Bayan wasu shekaru masu yawa:
Abubbuwa da dama sun faffaru, wasu masu daɗi wasu akasin hakan. Baba Huwaila Allah yayi mata rasuwa, Baba Shatu tsufa ya far mata. Itace ciwon idanu, itace ciwon sawu, itace tarin tsufa. Mahaifin Audu shima Allah yayi mishi rasuwa. Gidan a halin yanzu mune iyaye. Yaranmu sun girma harma an aurar da wasu. Shagari ɗan gidan Hindu, ƙanin Shatu yayi aure, Audu ya yanka mishi waje a cikin gida, ya gina ɗaki ciki da falo, suna zaune a gidan. Hannatu kuma tana gaban Hindun tana mata tallah. Ita kuma Zainab tayi aure a nan ɗan ƙauyen dake kusa damu. Sauran mazan kuma na Hindu, biyu daga ciki, sun gaji sana'ar mahaifinsu ta dambe.Auwal kuma bashi da aikin yi sai zaman majalisa, in damina tazo, yana taɓa aikin gona na kuɗi. Yarana kuma yanzu, Shatu dai tana aiki a wani kamfani a cikin Zamfara, Zaliha kuma, Lauya ce, Basira kuma tana aji biyu a jami'a tana karanta kasuwanci. Duk suna zaune a cikin gari, sun kama ɗaki, Shatu na kulawa dasu, kuma sun riƙe mutuncinsu sosai, sun taso da nutsuwa gami da kamun kai. Duk juma'a suke shigowa Ɗanbo, ranar lahadi da yamma kuma

sai su koma. Usman kuma kiwo yake yi na awakai, harma ya haɗa garke guda, da a gida yake yi, amma Hindu sai tasa mugunta, kullum saimu wayi gari dabba ta mutu. Saiya tattare awakanshi, ya mayar gidan abokinshi. Daga bisani kuma, wani Alh daya gina gidan gona a bayan gari. Saiya samu labarin irin yanda Usman ya iya kiwo saiya neme shi akan yazo ya dinga kula mishi da kifinshi da yake kiwo, da awakai. To Usman saiya roƙi Alhn nan ya kai awakanshi can gidan gonar, duk yake kulawa dasu, duk wata yana biyanshi. Duk da sana'ar man ƙuli da ƙuli na, na ɗauki ragamar karatun yarana kab. Usman da yaƙi karatun ya nuna mun ga abinda yake so, saina ɗauki kuɗi na bashi, ya siyo akuya, da bunsuru. Kamar wasa, akuyarnan taita haihuwar mishi, ƴan hurhuɗu, tashi ɗaya garke ya haɗu, saiya siyo rago da tunkiya, suma sukaita hayayyafa. Yaran gidan duk sun girma, matan da yawa suna gidan mazajensu."

Ina zaune a tsakar gida, ina baza gyaɗa, Shatu tayi sallama ta shigo, cikin shiga ta kamala, ko ina a jikinta rufe rub. Hannunta riƙe da ƙatuwar leda.

"Mama Aikin gyaɗa kike yi? Bayan kinsan duk ran juma'a da asabar muke yi miki in mun zo. Ki dinga hutawa. Baba Mariya ina wuni, Baba Hindu ina wuni?" Mariya ce kawai ta amsa, Hindu kuwa kunnen uwar shegu tayi da Shatu. Hannatu taja tsaki tace.

"Aikin banza, aikin wofi, bayan munsan komai, ana zaune a binni ana tazubas" wani abune ya caki ƙirjina dajin kalmar da Hannatu ta jefi yarta dashi. Duk da inajin ana jifansu da kalmomi iri_iri, cewar na barsu sun tafi karuwanci a birni, sunƙi aure, sai yawon ɓel_ɓel. Shatu tayi murmushi, ta girgiza kai, dan rayuwar da Hannatu take gudanarwa rayuwace ta abun tausayi. Shatu tace.

"Mama dama tafe nake da baƙo yana waje, yace lallai_lallai shi yana son ku gaisa. Oganane a wajan aiki, kuma muna mutunci sosai, yana yawan rage mun hanya" murmushi nayi, ina kallon Shatu wacce ta zama ƴar gaye, tamkar ba'a tsakar gidannan tayi rarrafeba. Wato shi ilimi har ƙarama mutum kyau yake yi, gashi da sa kwarjini.

Yi maza ki shigo dashi, kaji ƴar nema shine kika barshi a waje?" Dariya tayi mun, ta fita zuwa shigo da baƙon nata. Ni kuma na shiga ɗaki na shinfiɗa mishi ƙatuwar daddumar da Zaliha ta sai mun." Ina zaune sai na jiyo sallamarsu, baƙon Shatu na gaida mutan gidan. Da sallama suka shigo. Cikin girma da karamci muka gaisa, kansa a ƙasa cike da tsantsar jin kunyata. Nace.

Ya sunan malamin? A kunyace yace.

"Sunana Isma'il dama kullum ina cewa ta gaisheki, sai yau Allah ya nufa nace bari dai, inyi tattaki inzo mu gaisa, dan zuwa da kai yafi saƙo." Murmusawa nayi. Nace.

Zahiri Isma'il. Kuma naji daɗi Allah yayi albarka. Shatu bashi ruwa yasha mana" Fita nayi na dawo tsakar gida na basu waje. Ina zama Zaliha da Basira suka shigo, a jere tamkar tagwaye, komai iri ɗaya suka saka na sutura. Suna ajjiye ledojin hannunsu, suka shiga baza mun ɗanyar gyaɗar da nake aikinta." Buguzum_buguzum Audu ya shigo gidan, bakinshi duk dabzar goro, yana kumfar baki yace.

"Ina karuwar ƴarki naji ance ta tawo da daduronta sun shigo nan gidan ko? Duk lalatar da suke aikatawa a birni bai ishesu ba har sai sun kawo mun daduro cikin gida? Ke wato magajiya harda basu waje." Kallo nabi Audu dashi, raina bai taɓa ɓaci makamancin irin na yau ba. Amma bana son tanka mishi dan gudun kar hakan ya taɓa darajar Shatu. Hindu ta nuna ma Audu ɗakina da bakinta, karab a idanuna. Harya nufi ɗakina, ya dawo ya fisge ledojin da su Zaliha

suka shigo dashi ya zazzage. Kaji gasassu, da lemon roba ƙatuwa, da taliya, bushashahen kifi, da maggi, da farin mai, da tumaturin gongoni, da kayan abinci iri iri cimar ƴan birni ya gani sun zubo daga ledar nan. Baki ya rike, ya ɗauko kajin a ƙasa yace."

"Gaskiya naga kin sake, sai walƙiya kike yi. Ashe ribar bariki ake kawo miki. Ke Hindu zo ki tattare kayannan ki ajjiye mun a turakata. Yana kaiwa nan ya wuce fu zuwa ɗakina. Da mugun gudu Hindu ta iso gaban kayan, ko nauyin jikinta bata ji, ta hau kwashe kayan. Ni kuwa adda'a duk wacce tazo bakina furtata nake yi. Hawaye sai suntiri yake yi a kumatuna. Su Zaliha ma sunyi tsumu_tsumu tamkar an watsa musu ruwan zafi." Fisgo Ismail Audu yayi waje. Sai zabga mishi mari yake yi, tamkar ya samu maƙiyi a filin dambe. Jama'a aka taru, dan Audu sai kwakwaso yake ta faman yi, tamkar kaza mai ƴaƴa. Ismail da yaga Audu na shirin illatashi, aiba shiri ya zame, ya fice a gidan da fashashshen baki. Shatu ya shaƙo yana shirin illatamun ita. Kukan kura nayi na fisge Shatu a hannun Audu. Audu daya zuchiya, saiya rufeni da wani irin mahaukacin dukan da ko sanda nake da jini a jika bai taɓa yi mun irinshi ba. Faɗuwa ƙasa nayi hangurarriya ( sumammiya) Ban kuma sanin kaina ba, sai farkawa nayi na ganni a gadon asibiti, tsintsiyar hannuna ɗaure da ruwan bature. Fuskata tayi wani irin mugun nauyi, idanuna ma basa gani sosai, ko buɗuwa basa yi"

[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: *_🔥GAWURTATTU UKU🤟2023_*

*_TALLAH TALLAH  TALLA🗣🗣🗣🗣🗣_*

_A HAYYEH SAMAH MATAH💃💃💃💃💃💃_
*Ku shiga wannan link ɗin don zaɓar kaya masu rahusa👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/G6BmHCxso0rDZyWVQGgYYj
----------
No
07067964894

*_INA KUKE MATAN KWARAI MATAN DA SUKA AMSA SUNAN SU NA MATA A DUNIYA KU GARZAYO KUZO M A C DON ZABEN NA KWARAI KI DAURA ASAN KIN DAURA SAI ATAMFA DA LACE DA SHADDA, MATERIAL WITH SHOE'S AND BAG WITH JEWELRIES DAGA MAMAN ANNUR COLLECTION._*
*_ANAN KWALIYA ZATA MAIDA KUDINTA GAREKI,  KIFITO ASAN KIN FITO KIN FASA TARO SAI M.A.C  AKAN FARASHI MAI RAHUSA SAYEN NAGARI MAIDA KUDI GIDA IYA KUDIN KI IYA SHAGALINKI🤝_*
*_TANA KANO TANA AIKAWA KO INA DA IKON ALLAH A CIKIN AMINCIN DA YARDAN UBANGIJI_*
*_YAN UWA INA MASU SON SUYI SANA,A BASU DA JARI  TOH GA DAMA TA SAMU, INJI MAMAN ANUR DON ZAKU IYA DAUKAN KAYAN MU KU TALLATA KU DORA NAKU RIBAN SAMA ZAMU AIKA MAKU KAYA GA MAISHI DA SUNAN KU A DUK INDA CUSTOMER DIN KU YAKE BA TARE DA MUYI SAVING NO BASHI BA KUMA BA ZAISAN BA DAGA WURIN KI KAYAN YA FITO BA TAKEN MU GASKIYA DA AMANA,  MUM ANNUR

COLLECTION DA KARAMAR RIBA MUKA DOGARA SABODA NEMAN ALBARKA SAI KUN ZO 👏👏👏👏👏_*
[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: Gawurtattu uku,zasu buɗe aji na musamman da azumi,don koyar da girke girke na musamman na azumi don kun san mu mata ƴan adone,wajen yin girki in akace baki iya girki ba to tabbas mijinki fa kullum yana kan hanyar yawon restuarent, sannan idanuwansa suna kan ƴammata saboda ya samu sarauniyar girki, kada ki bari a barki a baya don gwangwaje me gidanki.

Domin nema ƙarin bayani,sai ku tuntuɓi waɗannan numbobin👇🏻👇🏻

07068606171
08104335144
08179523215

💃💃💃💃💃

*🤟GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARA TA 2023🤟*
*_Ina kuke masoyan gawurtattu uku ga su ssun dawo muku da wasu sabbin labaransu a wannan sabuwar shekarar, wannan karon salon gawurtacce ne, ku hanzarto kar ku sake ayi babu ku._*
_Sun shirya tsaf a wannan karon don kawo muku labaran da zakuyi fahari da su, tafiyar mai zafi ce sannan ta musamman._

*_Haziƙai kuma gawurtattu ukun sun shirya ne domin kawo muku gwarazan labaran da zaku yi alfahari da su._*

*MATA IYAYEN GIJI*
_Mrs Bukhari_

*INDA BA ƘASA..!*
_Ummu Maheer_

*KARO ƊAYA...!*
_Ummu Affan_

_LITATTAFAN GABAƊAYA AKAN FARASHI MAI SAUƘI DA RAHUSA 1K_

1 500
2 700

3 1000

_Kai tsaye zaku tura kuɗinku ta wannan account number ɗin._
2212328303
RABIATU BASHIR
Zenith bank

_Don Allah wannan karon ba ma buƙatar katin waya, idan baka da account to kaje POS ka bada 50 kob 100 a cikin kuɗin a turo ta account number please._

_Ƴan ƙasar Niger kai tsaye zaku turo ta nan._ 0706 860 6171

*DOMIN NEMAN ƘARIN BAYANI A TUNTUƁI ƊAYA DAGA CIKIN LAMBOBIN NAN.*

0810 433 4144
0817 952 3215
0706 860 6171

*MUN GODE DA KASANCEWA DA GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARAR 2023 SABON SALO SABON TAKU.*

_TEAM GAWURTATTU UKU 2023_

Mrs Bukhari[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: GAWURTATTU UKU

LAMBA TA GOMA SHA TARA
Saleri:

Musina:
Rayuwa kenan, a kullum inna zauna, sai inta kallon rayuwa, da yanda lamarin duniya ke tafiya, lallai tsarki ya tabbata ga ubangijin kowa da komai. Yanzu yanda muke jin zafin mutuwar iyayenmu da duk suka rasu, suka kwanta dama, haka muma wata rana yaranmu zasu tsinci kansu cikin maraici. Su Baba Hauwa an kwanta dama, mahaifin Yawale ya jima shi kam da rasuwa. Baba Sahura ce kaɗai ta rage. Ita kanta cikin ciwo take sai an kwantar sai an tayar. Yara duk sun zama samari, matan an auradda wasu, daga cikin mazan ma wasu sunyi auren. Awaliyya ta wajena, yanzu malamar asibiti ce, ɓangaren ƴan haɗari. Tana aiki a babban asibitin

dake jihar Bauchi. Haka kullum take zuwa ta dawo. Kulu kuwa karatunta iya sakandare ya tsaye, akayi mata aure, danta nuna mun auren ya fiye mata. Naso tayi karatu mai zurfi, amman bata bani haɗin kai ba. Tana aure a nan kusa damu. Kattume ma tayi aure, iyakarta itama sakandare, tana aure a can jama'are. Jamilu kuma manomine babba, dan Allah yasa albarka a hannunshi, duk abinda zai shuga, zai samu albarka mai yawa. Kasimu kuma, yana aiki a Azare, a wani kamfanin buga bulo. Mustapha kuma maginine, sai ƴar auta ta Zubaida. Itama da halama tana da burin yin zurfin karatu. Tana ajin farko a jami'ar A T B U nan Bauchi. Tare suke fita da Alawiyya. Sai dai wani sa'in Zubaidar tana zama a ɗakin ɗalibai, musamman in jarabawa ta matso."
Kumatu kuma Saminunta yayi aure, Yawale ya bashi fili a cikin gidan yana zaune da matarshi. Zakiya tayi aure a Kaduna, ta auri wani ɗan uwan Kumatun, hamshaƙin mai kuɗin gaske ne. Kamar dai yanda nake ji a bakin Kumatu da matan gidan kenan. Sauma'iyya kuma tayi auren amma yanzu zawarci take yi, auren ya ƙare. Muttaƙa kuma ya zama ɗan sara suka, sune ɓarayin kaji, da agwagin mutane. Su A'i duk sun aurar da yara. Sai ƴan tsirari da suke gabansu, amma ana shirin kawar dasu suma.

Ina zaune a tsakar gida ina yanka sabulu, Jamilu na ƙirgama wata wacce tazo sari a wajena. Ƙasimu yana gefen wajan ɗakina yana yi mun miyar kuɓewa bushashshiya, nayi tuwon tun kafin in zauna aikin yankan sabulun. Alawiyya da Zubaida kuma sun shiga cikin gari. Mustapha ne ya fito da wankin kayana a hannunshi. Jamilu na ganinshi da kayan ya tashi a guje ya nufi Mustapha, sai kace wani ƙaramin yaro.

"Wa ai wallahi baka isa ba. Gyaran ɗakin da kayi bai isheka ba, saika shigar mun aikina? Aini nake yin wankin duk sati inya taru." Mustapha na dariya yace.

"Amma naga kana taya Inna aikin sabulu, ga masu sari sunzo. Kaga ga wata ma ta shigo" Fur Jamilu yaƙi yarda saida ya fisge kayannan a hannun Mustapha ƙarfi da yaji.

Haihuwa mai rana. A rayuwar gidan Yawale da nayi sam babu daɗi. Amma gashi yau na haifi yara, sun share mun duk hawayena, suna bani dukkannin wata kulawar daya dace. Damuwata ɗaya ce, rashin waiwayarmu da Idi baiyi ba, sama da shekara ashirin da biyar, wannan itace kaɗai damuwata. In aka cire wannan, bani da wata damuwa da take damuna sam. Girgiza kai nayi nace.

Kai Mustapha tawo ka ƙirga mata, bar mishi aikinshi kaji. Ƙasimu sannu ɗan albarka"
Kumatu taja wani tsaki mai ƙarfi. Ni bansan ma ta fito ba, dan mu kaɗaine a tsakar gidan. Muttaƙa ne ya shigo a guje, ya bangaje Kumatu ta faɗi ƙasa warwars shi kuma ya shige ɗakinta."

"Wayyo hannuna, wayyo ƙafata" Da sauri na miƙe tsaye.

Kai Ƙasimu zo ka ɗaga Yadikkonku maza. Sannu Kumatu."
Da sauri Ƙasimu yaje ya ɗagata. Fadawan mai gari ne, suka shigo gidan da zabga_zabgar dorunanrsu.

"Muttaƙa muka biyo, kuma munga shigowarshi. Dan haka a fito mana dashi" Tsurewa Kumatu tayi. Ai su A'i iyayen gulma anajin haka sai gata ta fito tsulum.

"Bayin Allah ko me yayi haka, kuka biyoshi da waɗannan murtuka_murtukan dorunan? Kuma yana shigowa ya haure danga ya dire bayan layi" Cewar Kumatu kenan wacce take riƙe da hannunta da nake tsammanin zata iya samun tsagewar ƙashi tsabar buguwar data yi. Ni dai ina

tsaye ina mamakin Kumatu yanda duk ta gurɓata ma yaranta kab rayuwarsu. Haka fadawannan suka tafi, bayan sun faɗama Kumatu, akuyar mai gari suka sace. Kuma duk inda Muttaƙa ya shiga a ƙauyan zasu nemo shi. Suka fita suka barta da borin kunya. Sai zage zage take yi, harda kuka, ga hannunta dake ta faman zugi.

"Wallahi ni nasan hannu akasa ma Muttaƙa amma ba yin kanshi bane. Allah ya toni asirin duk mai sa hannu akan lalacewar yaronnan. Baƙin ciki akeyi mishi, anga ya taso da ƙarfi." Tsaki naja, nayi zamana naci gaba da aikina. Yarana bayan duk sun gama mun aikina, sai kuma ko wannensu ya nufi wajan sana'arshi.

Da yamma ina zaune ina haɗa sabulu, Yawale ya shigo cikin gidan da leda cike da cefane. Ya miƙa ma Kumatu.

"Ki gyare kayan miyannan Kumatu, kiyi mana jar miya. Kazar wajan Sauma'iyya ki yanka mana ita asa a miyar. Zan bata kuɗin. Bakinane sam babu daɗi so nake inci wani ɗan abu mai galmi, kwana biyunnan bana jin daɗin jikina, kasala da na damuna, gashi mamana na gefen hannun dama ya soma damuna da ciwo fa." Yawale na kalla nace dashi.

Sannu da dawowa Malam "

"Yauwa Musina ya kasuwar Dai"

Alhamdulillah" Ina faɗin haka nayi shigewata cikin ɗaki. Tuwo na zuba, da miyar kuɓewa taji naman rago, gashi naman yayi laushi. Ina ci ina shima yarana albarka. Jamilu ne yayo Sallama ya shigo. Hannunshi riƙe da leda cike da lemon taba_taba. Yasan inason taba_taba sosai musamman manyan da suka yi jawur a bishiya.

"Uwo ga lemon taba_taba na sayo miki. Bari in ɓare miki. Zama yayi a gefena ya soma ɓare mun.

"Uwo waini ya batun maganar Auren Yaya Kasimu ne, ni ranar Alawiyya na bani labarin wai kinje gidansu yarinyar da zai auran. Kuma magana ta faɗa, har Kawu Jamilu yaje ankai sadaki"

Gaskiya ne. Iyayenta dai sunce a bari sai watan cika ciki, in Allah ya kaimu. To Kawunku sun shige gaba anyi komai, an biya sadaki, dan Babanku yace bazai sa hannunshi ba. Lokaci kawai muke jira. Inason in samu Babanku da batun inda shi Ƙasimun zai zauna. Kila ya taimaka ya yanka mishi guri a kusa da Saminu. Sai Zaidu ya gina mishi. Jamilu yace dani.

"Uwo Baba Kumatu bazata taɓa barin Baba yayi mana abun arziki ba. Ita fa so take yaranta ace su kaɗai suka mallaki dukiyar Baba, gado ma dan tasan dole a raba da mune, kinsan da bazata yadda a raba da ƴan ɗakinnan ba. Amman ga shawara Uwo. Wannan filin nawa na unguwar madaki, mai zai hana Yaya Ƙasimu ya gina, yayi zamanshi acan kamar zaifi ko? Kuma filin yana da girma, dani da Mustapha duk zai ishemu muyi gininmu acan. Kinga shikenan kema saimu maidaki can kiyi zamanki tare damu, kema ki samu farin ciki. Amma mai kike gani?" Shiru nayi ina nazari. Abunda Jamilu ya faɗa gaskiya ne. Kumatu ba zata taɓa bari Yawale ya yanka ma Kasimu fili ba. Alhamdulillah yarana kansu a haɗe yake, kuma Jamilu yana samun kuɗi sosai akan amfanin gonarshi da yake siyarwa. Banda hatsin daya cika mana rumbu dashi, banda wanda yake raba ma matan gida da maƙota. Yanzu haka yana da gonakai biyu daya siya, ɗaya yana noma shinkafa, ɗaya yana noman riɗi a ciki. Banda gonakai na haya da yake haya. Dan ƴan uwanshi suna taya shi noman, harda su Alawiyya duk suna taimakon ɗan uwan nasu.

Maganarka gaskiya ce. Banso suka san da wannan filin ba ma Jamilu. Amman kamawa

tayi. Allah ya saka maka da alkhairi. Bari ya dawo sai in faɗa mishi, a samu a hankali a soma gini.
Ai kuwa hakan Akayi. Ko da Ƙasimu ya dawo, saina zaunar dashi na labarta mishi abunda muka tattauna da Jamilu. Duk sunji daɗi kuma sunyi na'am da shawararshi. Ba'a wani ɗauki lokaci ba Ƙasimu ya soma gininshi. Labari dai ya zagaye harya faɗa kunnen Yawale. Ranar afujajan ya shigo cikin gidan. Yana kwaɗa mun mugun kira. Saida gabana ya tsinke ya faɗi. Buzu_buzu ya shigo da uban gemu"
"Da gaske ne, Ƙasimu ne yake gini a unguwar madaki?" Murmusawa nayi nace."
E shine, Jamilu ne ya bashi filin ya gina iya inda zai zauna da iyalinshi" Kuta Yawale yayi yace.
"Duk girman filinnan na Jamilunne, ko iyakar inda yaba Ƙasimunne nashi? Kiyi magana mana, sai wani murmushin ɗaukar rai kike yi" Ai Kumatu na jin haka zuruf ta miƙe ta baro, ɓarzar dawar da take yi ta matso kusa da Yawale. Kallonsu nayi dukka nace.
Duka filin nashi ne, ai wannan ƙaramine ma daga cikin filayenshi, banda gonakai daya mallaka" Ba Kumatu ba ba, har Yawale saida ya kaɗu da abinda yaji nace, take ya soma kumfar baki.
"To baki isa ki raba mun kan yara ba wallahi. Duk ƙoƙarin da Kumatu ta dinga yi tun yaran na ƙananu dan ganin ta haɗe kansu, kinƙi yarda. Yanzu sabida kinason duniya ta zageni, wata na ya kama a ƙauyannan ace na kasa ba yarana fili suyi gini a gidana, saida suka je waje, shi yasa kika amince musu su fitan ko? Sabida munafukace ke ƴar iska, har yarona ya mallaki irin waɗannan uban kadarorin ace ni ubanshi bani da labari? Fili tabkeken gaske, wanda mai gari ne kaɗai yake da irinsu. Hawaye ya soma zubarwa. Kumatu ta cabke da cewa."
"Ka dena kuka Malam, Ai Musina bata ƙaunar zaman lafiya, shi yasa kullum cikin cusa ma baƙin ciki take. Yawale yace
"Dake da yaran naki duka, ina son ganinku a turakata bayan sallar isha" Wucewa yayi yana share hawayenshi. Girgiza kai kawai nayi na koma ɗaki abuna. Bayan sallar isha duk muka hallara a turakar Yawale, da yarana da yaran Kumatu.

[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: *_🔥GAWURTATTU UKU🤟2023_*

*_TALLAH TALLAH  TALLA🗣️🗣️🗣️🗣️🗣️_*

_A HAYYEH SAMAH MATAH💃💃💃💃💃💃_
*Ku shiga wannan link ɗin don zaɓar kaya masu rahusa👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/G6BmHCxso0rDZyWVQGgYYj
----------
No
07067964894

*_INA KUKE MATAN KWARAI MATAN DA SUKA AMSA SUNAN SU NA MATA A DUNIYA KU

GARZAYO KUZO M A C DON ZABEN NA KWARAI KI DAURA ASAN KIN DAURA SAI ATAMFA DA LACE DA SHADDA, MATERIAL WITH SHOE'S AND BAG WITH JEWELRIES DAGA MAMAN ANNUR COLLECTION._*
*_ANAN KWALIYA ZATA MAIDA KUDINTA GAREKI, KIFITO ASAN KIN FITO KIN FASA TARO SAI M.A.C AKAN FARASHI MAI RAHUSA SAYEN NAGARI MAIDA KUDI GIDA IYA KUDIN KI IYA SHAGALINKI🤝_*
*_TANA KANO TANA AIKAWA KO INA DA IKON ALLAH A CIKIN AMINCIN DA YARDAN UBANGIJI_*
*_YAN UWA INA MASU SON SUYI SANA,A BASU DA JARI TOH GA DAMA TA SAMU, INJI MAMAN ANUR DON ZAKU IYA DAUKAN KAYAN MU KU TALLATA KU DORA NAKU RIBAN SAMA ZAMU AIKA MAKU KAYA GA MAISHI DA SUNAN KU A DUK INDA CUSTOMER DIN KU YAKE BA TARE DA MUYI SAVING NO BASHI BA KUMA BA ZAISAN BA DAGA WURIN KI KAYAN YA FITO BA TAKEN MU GASKIYA DA AMANA, MUM ANNUR COLLECTION DA KARAMAR RIBA MUKA DOGARA SABODA NEMAN ALBARKA SAI KUN ZO 👏👏👏👏👏_*
[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: Gawurtattu uku,zasu buɗe aji na musamman da azumi,don koyar da girke girke na musamman na azumi don kun san mu mata ƴan adone,wajen yin girki in akace baki iya girki ba to tabbas mijinki fa kullum yana kan hanyar yawon restuarent, sannan idanuwansa suna kan ƴammata saboda ya samu sarauniyar girki, kada ki bari a barki a baya don gwangwaje me gidanki.

Domin nema ƙarin bayani,sai ku tuntuɓi waɗannan numbobin👇🏻👇🏻

07068606171
08104335144
08179523215

💃💃💃💃💃

*🤟GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARA TA 2023🤟*
*_Ina kuke masoyan gawurtattu uku ga su ssun dawo muku da wasu sabbin labaransu a wannan sabuwar shekarar, wannan karon salon gawurtacce ne, ku hanzarto kar ku sake ayi babu ku._*
_Sun shirya tsaf a wannan karon don kawo muku labaran da zakuyi fahari da su, tafiyar mai zafi ce sannan ta musamman._

*_Haziƙai kuma gawurtattu ukun sun shirya ne domin kawo muku gwarazan labaran da zaku yi alfahari da su._*

*MATA IYAYEN GIJI*
_Mrs Bukhari_

*INDA BA ƘASA..!*
_Ummu Maheer_

*KARO ƊAYA...!*
_Ummu Affan_

_LITATTAFAN GABAƊAYA AKAN FARASHI MAI SAUƘI DA RAHUSA 1K_

1 500
2 700
3 1000

_Kai tsaye zaku tura kuɗinku ta wannan account number ɗin._
2212328303
RABIATU BASHIR
Zenith bank

_Don Allah wannan karon ba ma buƙatar katin waya, idan baka da account to kaje POS ka bada 50 kob 100 a cikin kuɗin a turo ta account number please._

_Ƴan ƙasar Niger kai tsaye zaku turo ta nan._ 0706 860 6171

*DOMIN NEMAN ƘARIN BAYANI A TUNTUƁI ƊAYA DAGA CIKIN LAMBOBIN NAN.*

0810 433 4144
0817 952 3215
0706 860 6171

*MUN GODE DA KASANCEWA DA GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARAR 2023 SABON SALO SABON TAKU.*

_TEAM GAWURTATTU UKU 2023_

MRS BUKHARI
[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: MRS BUKHARI

GAWURTATTU UKU

LAMBA TA GOMA SHA TAKWAS:

Hawayene suke surnanowa ta gefen idona, suna sauka a matashin da kaina yake. Yau ni Audu ya daka a gaban yarana, da girmana yasa hannu yaimun dukan da har saida aka danganani da asibiti? Lallai na yarda Hindu ta shiga ta fita, ta cusa ƙiyayya mai ƙarfi a tsakanina da Audu. Duk da shima yana da nashi halin muguntar. Dan tun kafin Hindu tazo yake bani kashi. Shatu ce ta juyo, sai muka haɗa idanu. Kuka ta fashe dashi, wanda na kasa tantance na menene.

"Mama sannu kin farka? Basira maza kirawo mana likita, kice ta tashi. Jiki a saɓule Basira ta fita. Da idanu kawai nake binsu, ko ina ciwo da tsami yake yi mun a jikina.

Ina Usman Shatu?"

"Usman, yana gida, Kawu Ɗan lami yana jinyarshi, Shazili ya ƙarya mishi mishi hannu." Wasu irin hawayene masu ƙarfi suke ta ƙoƙarin makanta ganina. Har harshena yana sarƙewa nace.

Me ya haɗa Usman da Shazili, har abun yakai yake son durƙusarmun da yaro? Allah kana gani." Zaliha tace.

"Sabida ya riƙe hannun Baba sunyi kokawa, yana ƙoƙarin ƙwatarki, shine Shazili ya ɓalla hannun nashi. Kuma suka rufar mishi da duka, shi da su Yaya Shagari, da Auwalu. Yanzu haka mun shigar da ƙarar Baba Hindu, da shi kanshi Baban, da Shazilin. Kuma ni kotu zamu shiga. Zamu kwato muku hakkinku, kuma duk wani hakki da Baba ya tauye mana, zamu nemi kotu ta kwato mana hakkinmu. Lokaci yayi da baza mu iya zura idanu Baba da Hindu suci gaba da takaki ba. Ɗaukeki daga gidan zamuyi ma." Mari na dallama Zaliha, wanda saida yasa ta miƙe tsaye a zabure. Take tausayinta ya kamani. Nasan yarana sune gata na, na gode ma Allah daya bani aron lafiyar da na dinga neman kuɗi, badan komai ba, sai dan in haskama yarana hanya. Haƙiƙa ni kaina na ƙudurce a raina, ƙarshen zamana da Audu yazo kenan. Sai dai bazan so yaranshi su jashi a ƙasa ba. Duk lalacewar masa tafi ƙarfin kashin shanu.

Uban naku da matar uban naku, da ƴan uwan naku kuka miƙa sunayensu hannun hukuma? Ashe boko da sanin ƴancin kai shima hauka ne? Albaka nake fata kuyi a rayuwa, fatana ku rabu damu lafiya. Wannan jikin ya saba da wahalar Audu tun kafin kuzo duniya. Ku yi haƙuri ƴaƴana ku janye, in dai harni na tsugunna na haifeku." Basu da yadda zasu yi, dole suka ce dani sun janye. Kwanana shidda a asibiti aka sallameni. Babu laifi fuskar tawa ta ɗan saɓe. Kai tsaye su Zaliha suka wuce dani gidan da suke zaune. Suka kaini har gidan wata dattijuwa data kasance uwar ɗakunsu. Nayi ta binda da godiya. Muna zaune da daddare a falo, muna cin gashashshiyar kaza. Yarana sai jana da hira suke yi, burinsu suga ina walwala. Amman ina, sai dai na samar musu ƙirƙirarren farin ciki, badan yaudaraba sai dan in basu nutsuwa. Kwana na biyu a wajansu, muka dawo gida. Matan gida, da maƙota sai aukin sannu suke yi mini. Masu gulma nayi, masu zunɗe nayi. Hindu kuwa muna haɗa idanu ta fashe da dariya, ta shige ɗaki tana wani rausaya sai kace yarinya. Ɗakin da Usman yake jinya muka shiga. Yana zaune ana shafa mishi kitsen damo a hannun nashi. Ɗan Lami yana gefenshi. Sai aukin sannu muke ma juna ni da Usman. Saida mai maganin ya fita, Ɗan Lami ya faɗa ni da faɗa.

"Ke wacce iriyar shin me ruwa uku ce ( Sha_sha_sha) Yara suna son kwato miki darajarki, amma kina gwalesu. Kinfi sha'awar ciwon zuchiya yayi ajalinki kenan? Ya zama dole a shigar da ƙararnan. Dan wallahi abun ya isa haka tura kuma takai bango. To bari kiji abunda yake faruwa tun ranar da aka fita dake jina_jina a gidannan. Audu har fada yaje, ya bada sanarwar duk saurayi, ko tsoho, ko dattijon da ya shirya aure, ga yara a gidanshi kyauta, sadaki kawai za'a biya. Ba wannan bane abun mamakin ba. Wallahi har aka kwana aka wuni, babu wanda yace yanason waɗannan yara. Sai gulmace_gulmace aketa faman yi a gari, wai Shatu ta kawo daduro har gida. Hindu ta dinga bi gida_gida tana sake tabbatar ma da mata cewar kama Shatu akayi da daduro a ɗakin mahaifiyarta. Jibi abinda suka ma ɗanki, ke kanki jibi fuskarki. A wannan karon dole Audu ya sakeki." Goggo Rakiya wacce ta jima da tsaiwa a dokin ƙofa, kuma a kunnenta akayi bayanin komai tace.

"Ya zama dole ki yarda da abunda ƴan albarkar yarannan suka zo mana dashi. Da ba dan sunyi iliminba, da haka zaku zama ɗaya daga ke harsu, shin me ruwa uku kawai ( Sha_sha_sha) Zaliha kuyi abunda kuka saka a gaba. Allah yayi muku jagora, sai inda ƙarfina ya ƙare ni kuma" haka suka sani a gaba har saida na amince a maka su Audu a kotu ala tilas. Cikin kwana biyu, Zaliha ta dawo da takaddar sammaci. Ɗan lami, da Goggo Rakiya su suka tafi da sammacinnan har fada.

Ni kuwa koda muka dawo gida, jikina sam yaƙi dadɗi, ga tunane tunane da suka addabi zuchiyata. Ga habaice_habaicen Hindu wanda ta matsa mun lamda dasu a kwanakinnan. Audu kuwa sai sabgogin gabanshi yake yi, shi da Shazili gani suke zasu ci banza. Ƙuta nayi nace.

Mu zuba, inda dane bani da ƙarfin ramawa, bani da muryar da za'a saurari kukana. Yanzu karana ya kai tseko"

Fada:

"Allah ya taimaki mai gari. Wannan takaddar sammacice daga kotun birni. Ta Audu ce mijin ƴarmu, da Shazili, da Hindu, Yaranshi ne suka doka shi a gaban kuliya, suna neman a ƙwato musu hakkinsu dana mahaifiyarsu. Tun daga lokacin da aka haifesu har zuwa girmansu. Domun baisan komai nasu ba. Kuma ya cuskuna ma uwarsu ainun. Dan haka suna neman hakkinsu a wajan Audu." Goggo Rakiya na kaiwa nan, fada ta ɗauki tafi da sowa. Saida mai gari ya dakatar dasu. Ya dubi Goggo Rakiya yace.

"Rakiya, ni ina ganin da anyi sulhu anan fada ta da zaifi. Duk da nasan dolen Audu da Shazili su amsa kiran kuliya. Amma ya yara zasu kai ƙarar mahaifinsu? Shifa tuwo ba'a sauya mishi suna.

Goggo Rakiya tace.

"Amma in ba'a sauyama tuwo suna, ai hannunka yana ruɓewa ka je asibiti a yanke maka ko? To da kabarshi mana kaga in baici gangar jikinba duka." Fada tayi shiru kowa saida ya kaɗu da wannan lamari. Aka saka su Zaliha a gaba akaita tattaunawa a kansu, cewar baza suyi albarka ba." Mai gari ya tashi fadawa biyu yasa suyi mishi kiran Audu."

Audu:

Yana zaune yana shan fura, Hindu kuma tana gefenshi sai sake zuga shi take yi akan lallai, ko

a cikin gidanne tunda da samari, ya tursasa musu su auri su Shatu kowa ya huta."

"Damma baka zuwa sha'ani, da kaji yanda ake zagin Shamsiyya da ƙattin yaranta. Kuma abun takaicin, zagin har takan nawa yaran yake sakkowa. Yanzu Hannatu, mane minta cewa fa yayi in da gaske su Shatu yayyenta ne, bazai iya aurenta ba. Cikin dabara yanzu nake son tayi mun kiran yaron mu zauna mu tattauna" Audu yace.

"Shawararki mai kyauce sosai Hindu, ni kam nayi dacen samun mace mai hangen nesa. Aini ban tuno da samarin gidan ba, da bazan fita har dawa ina shelar masu aurensu ba." Sallamar  Salame suka jiyo a ƙofar ɗakin. Hindu ta amsa mata."

"Baban Shatu, mai gari ne ya aiko ayi kiranka. Manzannin suna waje"

"To gani nan Salame" Miƙewa yayi, yasa babbar riga, ya kifa hularshi.

"E bari inje ɗin Hindu, ƙila an samu wanda ya daki ƙirji zaiyi jahaɗin auren ɗaya daga cikin yarannan ne"  Yana kaiwa nan ya fita. Hindu ta sauke ajjiyar zuchiya na cin galaba akan raba Audu da yaran Musina data yi." Zainaba ce ta shigo cikin ɗakin hindu da kururuwar ihu, fuskarta duk a kumbure, da halama duka taci sosai."

"Ma'aikin Allah na madina ni Hindu. Haɗarin Bodi kuka yi ne Zainaba?" Cikin kuka tace.

" Fatsima ce tasa Tanimu ya rubuta mun takaddata saki uku. Kuma yace in tawo da yarana baya ƙaunar mu. Bayan tasa yayi mun mugun duka." Ɗiyar Zainaba ce ƙarama ta shigo mai sunan Hindu. Ga goyo ɗanye a bayan Zainaba."

MRS BUKHARI[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: MRS BUKHARI
GAWURTATTU UKU

LAMBA TA ASHIRIN"

INA MIƘA ƊUNBUN GODIYATA S GAREKU MASOYA RUBUTUNA. HAKIKA WANNAN LABARIN YA KAINI WANI MATSAYI DA MATAKIN DA BAN TAƁA TUNANIN ZAI KAINI BA. HAJIYA TURAI NAGA SAƘO INA GODIYA MAI TARIN YAWA.

YAWALE:
Ƙarema yarana kallo yake yi. Masha Allah ko wanne cikinsu ya ginu da tarbiyya, gasu da mugun haɗin kai da soyayyar junansu. Gashi kowa yana da abun hannunshi. Yaran mowa Kumatu kuwa, Saminun ne dama dama a cikinsu, amma du sauran basa sana'a sai yawon ɓel_ɓel da bin inuwa. Muttaƙa kuwa yayi nisa baya jin kira. Yanzu haka yana can a kulle a kurkukun bayan gari, mai gari yasa an kamoshi shi da abokan satar tashi, ya garƙamesu a mari. Babu irin bori da tumamin da Kumatu bata yi ba a tsakar gida."

"Musina nayi mamakin abunda kike shirin sa yarana suyi. Wata kam ba kya ƙaunar kiga muna zaune lafiya. Shin me Kumatu tayi miki da kika ƙi jinin yaranki su haɗe kansu da yaranta? Duk abinda yaranki suka kawo miki sai dai kici ke kaɗai. Kin nuna musu banda galihu a wajanki, kuma baki basu tarbiyyar su kula da Yadikkonsu Kumatu ba. Wai dam ɗiban albarka har Jamilu

ya mallaki garjejen fili a ƙauyannan amman ni ubanshi banda labari Musina, ga gonakai daya mallaka da sa hannun mai gari amman ni ina nan hoto jibi yanda na dawo dan tsabar wahala komai nawa ya ƙare, dan baƙin hali yarana dana arziki amman kin hana su taimaka mun. Wallahi zan kafa dokoki a gidannan kuma dole abi, zaman zai sauya ko dan haɗin kan yaranmu. Ni dai bance uhm ba, bare um_um jira nake ya gama zazzago duk abinda yake cikinshi tukunna, su Jamilu sunyi tsuru_tsuru suna kallon mahaifinsu, ba'a taɓa yin zama irin wannan ba a gidannan sai yau.

"Daga yau duk abinda yaran wajanki suka siyo suka kawo miki, na ci, ko sutura, to dole su siyo da Yadikkonsu, in basu da halin yi muku duka, sai suyi haƙuri. Nan Alawiyya take wucewa da babban buhu shaƙe da kayan alatu, bushashahen kifi a miyarki kamar zaiyi magana, amman baki basu tarbiyyar su kula dani ba. To itama duk wata inya ƙare duk abinda ta siyo a raba da Kumatu. Jamilu da yake ɗiban hatsin da bai wuce rabin buhu ba ya bamu, shima na soke dole ya raba duk hatsin daya samu gida biyu, rabin a rumbunki, rabi a rumbun Kumatu bayan ya ware na siyarwa.  Kema Kulu inajin labarin jar biya da kike kawo ma uwarki cike da zabi duk wata. Daga yau ko ki haɗa da Kumatu ko ki bari.Ita kanta Kattume ƴar gatan uwa da tana wajan zamannan wallahi saina bigeta ma, dan inajin hidin_dimun da take yi ita da mijinta a gidannan, amman dai_dai da hatsi baki taɓa bari ta auno bata Kumatu ba.  Sannan Alawiyya da Zubaida duk su fitar da mijin Aure na gaji da ganinsu a gabana anayi mun ɗan kallo a gari. Wani iri numfashina yake yi, da ba dan yara ne a gabanmu ba, da yau Yawale yaga hau irin namu na masu haƙuri. Waigowa yayi wajan su Jamilu da suke jere da Saminu.

"Kai Jamilu na haɗaka da Zulai ƴar wajan Yayana Jamilu ka aureta, mun gama maganar da Yaya Jamilun, tuwona maina. Kai kuma Mustafa sai ka auri marka yarinyar Mudi duk a haɗe ayi auren dana Kasimu. Ke kuma Sauma'iyya mun gama magana da Zaidu zai aureki ya haɗaki da Harira zaki ci gaba da zama a cikin gidannan. Gida bai ƙoshi ba baza'a kaima dawa ba. Alawiyya, Zubaida, ku fidda mijin aure nanda mako guda in ba haka ba. Akwai samari fal gidannan zan tilasta musu su aureku, duk da baza su so auren fitsararru irinku ba. Kasimu ka samu Saminu zai yankar maka fili, kuma Jamilu ku sameshi a yanka muku." Kallon Yawale kawai nake yi, ko kunya baya ji sai hukunci yake zartarwa akan yarana dana gama wahala akansu. Har yake tunanin haɗa Jamiluna da Zulai yarinyar data zubar da ciki watan jiya, yawon bin maza take yi kwararo_kwararo. Ita kuma Marka ba ƙaramar fitsararriya bace, dan ko aiki,ko aike uwarta bata isa ta sanyata ba, sune za'a aura ma yarana, dan anga Allah ya tallafi rayuwarsu komai ya wuce rayuwa tayi mana shar. Su Jamilu sai kallona suke yi, kallo irinna kiyi mana rai. Ni dai Yawale da Kumatu nake kallo kawai, cike da maɗaukakin mamaki.

"Sannan Kumatu zanci gaba da muku rabon kwana ke da Musina, kuma duk nauyinta dake kaina zan sauke mata, fatana ku zauna lafiya.'

Kutumar bura ubanka, Yawale kaine kake faɗen haka da bakinka?" Bansan sanda bakina ya subce na narko wannan ashariya a gaban yara ba. Duk suka kalleni, nayi maza na sauke kaina. Yawake kuwa sai murmusawa yake yi, babu halamar fishi ko tunzura akan ashariyar dana narko mishi. Kallon su jamilu yayi yace.

"Ku tashi ku tafi, na sallameku Allah yayi muku albarka, ayi haƙuri kuma a yafi juna. Komai ya wuce yaran kirki" sai washe baki Yawale yake yi, nasan dukiyar hannunsu yake kallo kawai. Ina kallo yaran suka watse, ai fitarsu ke da wuya na miƙe.

Yawale bari kaji in faɗama, aure ni da kai ya ƙare daga yau, yau kaji kana son ka sake

mayar dani matarka, sabida yarana sun samu arziki. Ni kuma ina baƙin ciki kaci dukiyarsu. Har hake cewa wai duk abinda suka kawo mun su ba Kumatu. Da kai da Kumatu Allah ya tsine muku albarka, ƴan iska, ƴan kutumar uba. Kuma wallahi babu ɗana guda ɗaya da zaiyi aure a zuriyarka. Yarona daya salwanta sanadiyyar sharrin da Kumatu tayi mishi. Bazan yafe ba, sai wutar Allah ta ciku." Da Yawale da Kumatun duk baki suka buɗe suna kallona. Dan na fusata ainun, shi kuma Yawale sai lallashina yake yi, sabida yana son cin banza. Kumatu tace.
"Musina Yawalen kike zagi haka? Wani mugun kallo na jefa mata nace.
"Dake dashi kun yayimi ƙwanyar bura ubanku, wakilin ɗaurin aurenku yaci uwatai. Haka na fice a ɗakin kamar kububuwa, ina huci dan jikina har kyarma yake yi mun, na koma nawa ɗakin. Duk yaran suna tsaitsaye sunyi cirko_cirko. Su kansu basu taɓa ganina a cikin irin wannan yanayin ba. Hakanne ya tilasta musu yin shiru, gudun karsu faɗi wani abun da zai kuma tunzurani. Kulu ta kasa tafiya gidanta, da dukkan halamu kwana zata yi, matan duk suka baibayeni"

Mrs Bukhari
[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: GAWURTATTU UKU
Lamba ta Ashirin da ɗaya

BAKORI:

Laila:
Da idanu nabi Shehu ina karantar yanayinshi kawai.
"Laila tunda babu gaisuwa ina wuni" murmushi nayi mishi, na miƙa mishi Ɗahiru, yasa hannu ya karɓeshi yana kallonshi, take sai fuskarshi ta sauya, daga fara'a zuwa akasin hakan.
Ina Wuni Shehu, kazo lafiya?"
"Lafiya lau Laila. Kuma na fito jeji lafiyar Allah, harma an zaɓeni a matsayin wanda za'a bama kujerar sarkin mafarauta, har an saka rana. Sai dai ina fargabar abunda kaje kazo, sabida wannan yaron naki, zai iya kawo mun cikas a mulkina. Hakanne yasa zan ƙara aure Laila, harma an saka bikin namu, saura kwana goma cib." Banyi mamakin auren da Shehu yace zauyi ba, maganganunshi sunfi bani mamaki gaya. Auren mace sama da ɗaya haka addininmu yazo dashi, muddin in miji zai iya adalci a tsakani. Malam bahaushe yana girmama lamarin ƙarin aure sosai, musamman ga mu ƴan ƙauye, dan ɗan ƙauye iyakar jin daɗinshi ya ƙare a kwanciyar aure da mace ne, shi yasa suke girmama dare. Balle Shehu da yafi ƙarfina, dan nayi imani Shehu yafi ƙarfin mace biyu ma. Amma aurennan babu makawa zaiyi ne danya mayar dani bora, an gama canfani cewar ni mai farar ƙafa ce.
Allah ya sanya alkairi. Na taya ka murnar cin nasarar zama zakin mafarauta. Aure kuma Allah ya bamu zaman lafiya. Ina neman alfarma Shehu."
Jin ban ɗaga hankalina ba yasa Shehu ya sassauto.
"Ina jinki Laila" Nisawa nayi cikin ɗacin rai da ƙunan zuchiya nace.
Saura kwana goma muyi arba'in ina son ka ƙara mun kwana goma akai, sabida zanyi ziyare_ziyaren dangi na. Har can Dutsin ma nake son zuwa wajan Baba Kande." Kai ya sosa yace.

"Babu komai, zaki iya ƙara kwana goma akai ma, baki da matsala. Karɓeshi ki kwantar dashi, ni zan koma." Hawayen da nake dannewa ya zubo mun, ganin yanda yake nuna halin ko in kula akan Ɗahiru. Nasan ni da Ɗahiru cikin garari zamu yi rayuwa a hannun Shehu, ga aure zaiyi sabida ya samu kwanciyar hankali a wajan matar da zai aura. A tunaninshi ma na gama tashi a aiki, tunda ya gama buɗani, ya nakasa mun ƙafata, tawa ta ƙare ko? Hmm maza mutanen mu ( Allah ya gafartama Aisha Ɗan kano) Kallona yayi yace.

"Hmm Laila kenan, ashe ba zaki godemun ba dana zaɓi in ƙara aure ba tare dana sakeki ba? Kinsan irin iftila'in dazai shafeni a sanadiyyar wannan abun da kika haifa kuwa, baki da labarin yanzu haka a gida, amma daina sayen kayan siyarwan da su Baba suke sayarwa, sabida baza'a iya aiko yara ba, shine har kina da idanun kuka dan zan ƙara aure, me yasa mata baku da adalcine ku, baza ku tausaya ma maza ba?" A al'adance laifine babba in ɗago in kalli Shehu ma a yayin da yake cikin fishi, in kuwa na mayar mishi da martani, tamkar na aikata wani zunubine mai girma. Dole na haɗiye maganganun da Shehu ya dinga yaɓa mini, a wajen ya fita ya barni, Ɗahiru na rungume a hannuna. Ina jiyo Shehu na gaisawa da Malam daya shigo yanzu.

Shehu:

"A Shehu kaine a tafe da rana haka?" Cewar malam. Shehu cikin girma da ladabi ya gaishe da malam, yake kuma labarta mishi batun zaiyi aure nan da kwana goma. Su Daddo suna tsakar gidan suna jiyo su. Malam yace.

"Naji labarin a wajan Buba, dan jiya na shiga Dutsin ma ɗin naje cin kasuwa. Kuma ya labarta mun komai. Fatanmu yarannan Allah ya basu zaman lafiya a tsakaninsu kawai. Ina taya ka murna Sarkin mafarauta" Dariya da Shehu da malam suka saka, yayi musu sallama ya fita.

Ta Asibi:

"Malam ni na kasa gane wannan zarwancen da kuke yi da Shehu fa" Murmushi Malam yayi, tare da nufosu. A gefensu ya samu waje yaima kanshi mazauni.

"Auren da Shehu Zaiyi ba kowa zai Aura ba, sai Asiya ƴar Kande ƙanwarki Ta Asibi. Malam Buba mahaifin Asiyan ya shaida mun, wai sunfi shekara guda suna nema. Shehun ya auri Laila da kaɗan suka soma nema. Abunda Allah ya nufa, Annabi sai ceto. Daddo tace.

"Asiya dai ɗiyar ƙanwar Yaya uwa ɗaya uba ɗaya, ita Shehu zai aura Malam? Ai ana barin halas dan kunya, duk matan da suke a gari, baiga wacce tayi mishi ba sai Asiya, yarinyar da taje birni ta gama buɗe idanunta a gidan aiki da aka kaita. Ta Asibi tama rasa tacewa, ta rasa dalilin da yasa ƴar uwarta bata ƙaunar farin cikinta, gashi su biyu rak iyayensu suka haifa. Taso ta Auri malam Zangina dan taso ta ribaceshi ya jiya ma Ta Asibi baya. Amma da yake yafi sha'awar mace mai alkunya ne yasa yaima Kande tawaye. Da bata samu hakan ba saita ƙulla zazzafar gaba da ƙiyayya a tsakaninta da ƴar uwar tata. Ta Asibi kasancewar itace babba, sai taita yin haƙuri da halayyar Kande, taci gaba da janta a jika, taci gaba da ziyartarta tana kuma yi mata alkairi. Shine daga baya ta saki jikinta, ashe ta ciki na ciki. Baƙin ciki Ta Asibi ta dinga haɗiya. Malam yace.

"Ta Asibi naga kin ƙume, abinda nake so dake shine. Kuyi haƙuri ku duka, kuma ku taushi zuchiyar Laila ta daure tayi ma Shehu biyayya akan auren ƴar uwarta da zaiyi. Taci girma ta kame kanta a matsayinta na babba. Kuma, ku daure karku nuna ma Kande wani abu na

sosuwar rai, gudun lalacewar zumuncinku, da Laila da Asiya duk naki ne. Abinda Shehu yayi ba laifi bane, tunda ba Allah ya saɓa ma ba. Sai dai yin hakan ya kaucewa al'adar malam bahaushe mu da aka sani da yakana da alƙunya. Kande zata zo yau haka Malam Buban ya faɗa mun." Yana kai aya ya kurkure bakinshi da ruwan buta yaja langar abincinshi, ya soma cin gwaɗon zogale. Bai idasa gama cin zogalennanba saiga sallamar Kande da ɗan buhun kayanta a ƙunshe, Asiya na biye da'ita. Ta Asibi ta kallesu dukkansu tana jin wani zafi da zugin Kande. Malam Zangina ne yai mata ido, saita ɗan saki fuskarta.

"Kande kune tafe a kwanɗeɗiyar ranar nan? Maraba lale, sannunku da zuwa Asiya" Cewar Daddo kenan dan Ta Asibi ta kasa iya sarrafa harshenta balle tayi musu sannu da zuwa. Kande ta ya da buhun kayanta, tana faɗin.

"Wash Allah makashin kakata Rakiya. Malam Zangina yau baka fita kasuwar bane?" Cikin girma yace.

"Nafita. Abinci dai nadawo inci, sai in koma Jafaru shima saiya je yaci. Sannunku da Hanya." Gaggaisawa akayi dukka. Malam Zangina ya wanke hannunshi, yai musu sallama ya fice."

Laila:
Ina tsaye ina share hawayena, na jiyo shigowar Inna Kande, kasancewar tana da ƙarfin murya. Da sauri nashare hawayena. Na shinfiɗe Ɗahiru na fita.

Inna kune a tafe? Asiya hmm ai nayi fishi wallahi kuwa" Kusa da Inna Kande naje na zauna,muka gaggaisa. Baki ɗaya saina kasa gane ma Asiya dan ko fara'a taƙi yi mun. Saɓanin da, da in muka haɗu tamkar zamu cinye junanmu, hira kuwa sai mun raba dare munayi. Saita tunomun zance da take rakani wajan Shehu in yazo, muita wasa da dariya. Maganar Inna Kande ce ta katse mun tunanina.

"Laila ashe mata maza kuma muka samu? Kaik abun baiyi daɗi ba. Dan samuwar yaronnan zai iya taɓa duniyarki, an riga an canfa irin haihuwarsu." Dam gabana ya faɗi har nake jin hawaye na shirin subce mun. Daddo tace.

"Wannan duk canfinmu ne Kande na malam bahaushe. Ba wani abunda zai samu Laila sanadin haihuwar yaronnan sai alkhairi. Ke Laila shiga ɗaki jikinki ɗanye ne. Yanzu ma zanzo muyi wanka. Kici gaba da kwanciya a gadon ƙasannan." Jikina a saɓule na miƙe, kobi ta kan Asiya ban sake bi ba.

Ta Asibi:
"Sai muka ji biki Malam yana shaida mana, ashe Asiya Shehun Laila zata aura? Shehunma bai jima da tafiya ba. Allah ya sa gidan zamanta ne" Cewar Ta Asibi kenan. Kande duk rashin kunyarta sai taji nauyi ya rufeta, nan ta shiga kame_kame dasokiburutsun zance"

"To ya zanyi. Buba ne ya ɗaure mata gindi. Har duka nayi mata, amman ta kafe sai shi. Wai tun lokacin bikin Lailan suka soma maganar aure. Yaya Abinda Allah ya nufa saiya faru. Masu iya magana sukance matar mutum. Shine na tawo da'ita zan kaita wajan Laraba ta zauna a can, ta dinga yi mata ƙunzugun lalle. In yaso in bikin ya rage kwanaki, saiki tawo da'ita Yaya" Da Daddo da Ta Asibi sun sha ruwan mamaki. Amman haka suka kanne, Kande ta kwana washe gari ta juya. Ta Asibi ta ɗauki Asiya ta kaita gidan Laraba. Kwananta bakwai a gidan Laraba, ana takwas ne Ta Asibi dasu Nazeefa suka ɗunguma zuwa Dutsen ma dan gudanar da biki.

Laila tana nan gaho bata san wa Asiya zata aura ba. Har sai bayan da aka kammala biki Amarya ta tare a ɗakin angonta. Sannan suka zaunar da Laila dan faiyace mata halin da ake ciki.

Laila

Mrs Bukhari

[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: *_🔥GAWURTATTU UKU🤟2023_*

*_TALLAH TALLAH  TALLA🗣🗣🗣🗣🗣_*

_A HAYYEH SAMAH MATAH💃💃💃💃💃💃_
*Ku shiga wannan link ɗin don zaɓar kaya masu rahusa👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/G6BmHCxso0rDZyWVQGgYYj
----------
No
07067964894

*_INA KUKE MATAN KWARAI MATAN DA SUKA AMSA SUNAN SU NA MATA A DUNIYA KU GARZAYO KUZO M A C DON ZABEN NA KWARAI KI DAURA ASAN KIN DAURA SAI ATAMFA DA LACE DA SHADDA, MATERIAL WITH SHOE'S AND BAG WITH JEWELRIES DAGA MAMAN ANNUR COLLECTION._*
*_ANAN KWALIYA ZATA MAIDA KUDINTA GAREKI,  KIFITO ASAN KIN FITO KIN FASA TARO SAI M.A.C  AKAN FARASHI MAI RAHUSA SAYEN NAGARI MAIDA KUDI GIDA IYA KUDIN KI IYA SHAGALINKI🤝_*
*_TANA KANO TANA AIKAWA KO INA DA IKON ALLAH A CIKIN AMINCIN DA YARDAN UBANGIJI_*
*_YAN UWA INA MASU SON SUYI SANA,A BASU DA JARI  TOH GA DAMA TA SAMU, INJI MAMAN ANUR DON ZAKU IYA DAUKAN KAYAN MU KU TALLATA KU DORA NAKU RIBAN SAMA ZAMU AIKA MAKU KAYA GA MAISHI DA SUNAN KU A DUK INDA CUSTOMER DIN KU YAKE BA TARE DA MUYI SAVING NO BASHI BA KUMA BA ZAISAN BA DAGA WURIN KI KAYAN YA FITO BA TAKEN MU GASKIYA DA AMANA,  MUM ANNUR COLLECTION DA KARAMAR RIBA MUKA DOGARA SABODA NEMAN ALBARKA SAI KUN ZO 👏👏👏👏👏_*
[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: Gawurtattu uku,zasu buɗe aji na musamman da azumi,don koyar da girke girke na musamman na azumi don kun san mu mata ƴan adone,wajen yin girki in akace baki iya girki ba to tabbas mijinki fa kullum yana kan hanyar yawon restuarent, sannan idanuwansa suna kan ƴammata saboda ya samu sarauniyar girki, kada ki bari a barki a baya don gwangwaje me gidanki.

Domin nema ƙarin bayani,sai ku tuntuɓi waɗannan numbobin👇🏻👇🏻

07068606171
08104335144
08179523215

💃💃💃💃💃

*🤟GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARA TA 2023🤟*
*_Ina kuke masoyan gawurtattu uku ga su ssun dawo muku da wasu sabbin labaransu a wannan sabuwar shekarar, wannan karon salon gawurtacce ne, ku hanzarto kar ku sake ayi babu ku._*
_Sun shirya tsaf a wannan karon don kawo muku labaran da zakuyi fahari da su, tafiyar mai zafi ce sannan ta musamman._

*_Haziƙai kuma gawurtattu ukun sun shirya ne domin kawo muku gwarazan labaran da zaku yi alfahari da su._*

*MATA IYAYEN GIJI*
_Mrs Bukhari_

*INDA BA ƘASA..!*
_Ummu Maheer_

*KARO ƊAYA...!*
_Ummu Affan_

_LITATTAFAN GABAƊAYA AKAN FARASHI MAI SAUƘI DA RAHUSA 1K_

1 500
2 700
3 1000

_Kai tsaye zaku tura kuɗinku ta wannan account number ɗin._
2212328303
RABIATU BASHIR
Zenith bank

_Don Allah wannan karon ba ma buƙatar katin waya, idan baka da account to kaje POS ka

bada 50 kob 100 a cikin kuɗin a turo ta account number please._

_Ƴan ƙasar Niger kai tsaye zaku turo ta nan._ 0706 860 6171

*DOMIN NEMAN ƘARIN BAYANI A TUNTUƁI ƊAYA DAGA CIKIN LAMBOBIN NAN.*

0810 433 4144
0817 952 3215
0706 860 6171

*MUN GODE DA KASANCEWA DA GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARAR 2023 SABON SALO SABON TAKU.*

[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: MRS BUKHARI
GAWURTATTU UKU

LAMBA TA ASHIRIN DA BIYU

LAILA:

"Laila ki buɗe kunnanki da kyau kiji me Daddonki zata faɗa miki. Kuma kiyi haƙuri da dukkannin abunda zaki ji." Innata tana kaiwa nan saita fice. Ni kuma jikina har rawa yake yi tsabaragen kaɗuwa, dama a daren jiya da aka ɗaura auren Shehu banko iya runtsawaba. Yanzu na gane dalilin matan da suka kasa tawakkali dan mijinsu ya ƙara aure, suyi hauka. Zafi da ciwon kishi, iyayen gida ne kaɗai ka iya ɗanɗana harsu gane abunda nake nufi ( Su maman Khairat,Deezatu ai baza su gane me nake nufi ba. Maman Yaseer ce kaɗai za tai mun uziri)

"Laila" Daddo ta kirayi sunana da harshe rarrauna."

"Shehu yayi aure har ya wayi gari a ɗakin amaryarshi. Abunda zamu ɗauraki akai shine haƙuri da juriya. Mai haƙuri shi kan dafa dutse har yasha romanshi. Ni da gyatumarki kina gani babu abunda yake shiga tsakaninmu na husuma. A tsakanina da'ita girmamawace, dan sanda aka auroni, shekaruna goma ina cikin na sha ɗaya. Ita da mahaifinku suka taru suka raineni. Kinsan dama ko mu jima, ko mu daɗe Shehu dole zai ƙaro aure. Ballema da kika haifi Ɗahiru kinsan yanda ƙabilarmu ta malam bahaushe ta canfa yara irinsu Ɗahiru. Babban abunda zan daɗa miki dashi shine, ki rungumi yaronki karki hofantar dashi, dan babu mai kula miki dashi, saike. Ki dage ki ta mishi adda'a ko Allah zaisa rayuwarshi tayi albarka. Ba kowa Shehu ya aura ba face Asiyan Kande ƴar uwarki. Amman ki daure ki jure zama da'ita Ta Asibi tace in horeki karki kuskura ki lalata musu zumuncinsu." Hawaye ya gama wanke mun fuskata har ɗiga yake yi. Sai yanzu nake tuno irin kallon da Shehu ke jifan Asiya dashi, sau tari ina kama Shehu na jifan Asiya da murmushi. Kasancewar ƴar uwatace ban taɓa kawo komai a raina ba ashe Shehu aurenta yake son yayi. Naji zafi ainun dan kwanana biyu ina cikin ruɗu da damuwa. Saida malam yaita mun nasiha sannan na dangana. Yaya Nafi matar wanmu ita taita zagawa dani yawon arba'in. Munyi ziyare_ziyare sosai. Bayan mun dawo kuma na soma shirin komawa, duk

da a cikin fargaba nake, dan bansan me zan tadda a gidan ba. Na shirya tsab, Goggo Laraba da Yaya Nazeefa da Anty Nafi sune sukai mun rakiya. Ina sa ƙafa a cikin gidan gabana ya yanke ya faɗi, su Iyami suka shiga jaye yaransu ƙananu. Su tsaya ma mu gaisa, sai daga nesa_nesa. A ɗakin Baba mai riga muka yada zango.

"Kune a gari Laraba, sannunku da zuwa"

"Yauwa sannunmu Mai riga, ga Laila mun dawo muku da'ita yadda kuka bamu haka muka dawo muku da'ita. Ya akaji da taro?" Baba mai riga ta yashe baki tace

"Taro ya watse lafiya. Sauran dangin mahaifin Shehun ma suna can ɗakin matar Malam basu tafi ba. Laila ya Ɗahirun?" Yaya Nazeefa tace.

"Me gidanki lafiya lau, yayi mul_mul dashi. Ni dai kaina a ƙasa har muka miƙe. Ɗaki_ɗaki na leƙa aka sake gaggaisawa. Sannan muka shigo ɗakina.

"Yanzu Laila ni inaga bari muyi miki kwalima, tunda sai gobe zamu juya, mu sake miki fasalin ɗakin. Saiki sake labulen da Inna tayi miki. Ni dai ina zaune sai tunani nake faman yi. Su kuma gadan_gadan suka shiga aiki. Sai bayan Isha suka game komai. Har zuwa lokacin Shehu bai leƙo ɗakin ba. Kuma ina jiyo muryarshi, yana kaɗa yara. Idanu na lumshe, a yanda naga rana haka naga dare. Sai jefin asuba na samu nannauyan bacci ya ɗebeni. Da sassafe su Yaya Nazeefa suka soma shirin tafiya. Goggo Laraba tace.

"Taso muje ɗakin Asiyan mu gani, tunda ita bata da kunya ta kasa yi miki sannu da zuwa" Idanu na gwalalo nace.

Goggo me yasa zamu je, ita da Shehun duk sun san mun dawo fa, amman ba wanda yazo ya duba mu." Sai tace.

"Ke dai ƴannan muje, ki daure ki cusa mata aniyarta." Haka suka sani gaba muka shiga, Asiya kamar babu wata dangantaka a tsakaninmu da'ita haka tayi mana. Goggo Laraba tayi mana nasiha, ni kuwa sai ƙarema Asiya kallo nake. Ashe banda komai ba. Wasa_wasa na zama bola a gidan Shehu, sai Shehu ya ishi Asiya yake zuwa ya nemi hakkinshi. Babu zancan rabon kwana sam. Ni kuwa haka na dinga kannewa inata jure duk wani abu dazai ɓullo. Ɗahiru kuwa na mayar da hankali kan renonshi. Tani da kishiyoyinta kullum a cikin faɗace_faɗace da gore_gore suke. Kawu Ɗahiru kuwa ya zama shahararren malamin da ake ji dashi, dan aikinshi tamkar yankan wuƙa haka yake. Kullum gidan a cikin baƙi mata yake, kullum sai an yanka kaji an soya anyi sadaka. Rayuwa taita tamaule damu, Asiya taita baza mulki a zuchiyar Shehu, dan ko fishi tayi dashi, ranar bashi ba sukuni sam. Ranar naɗin sarautar Shehu ta zagayo, amma ko labari banji da wuri ba, sai ana jibi za'ayi taron. Haka na auni alkama, da farar shinkafa, na kaima Sha'awa ƙawata, tai mun nakiya da alkaki, ko wanne fanteka ɗaya. Ranar naɗin sarautar naci ado cikin yadin banbalasta fari sol, nasha ƙunshi da kitso. Da safe bayan isowar su Yaya Nazeefa, saita raka ni naje har ɗakin Asiya na kaima Shehu tawa gudunmawar. Ganin haka sai yaji kunya, yana sanye cikin kayan saƙi, jikinshi cike da layu da guraye, Asiya taci ado da yadin tentalan, tana gefen hannun Shehu.

"Kiyi haƙuri Laila, Asiya zansa a naɗa a matsayin mai sauraron koken matan mafarauta, a matsayina na sarkin mafarauta, kinga ita ta'iya rubutu da karatu, ke ko ba ki iyaba. Naji ciwo, idanuna yai rau_rau, amman saina cije. Nace dashi.

Ai babu komai Shehu, duk dai abinda ka yanke yayi, kaine shugaba, Allah ya taya riƙo shine fatana." Yaya Nazeefa ta kamo hannuna muka fice. A taƙaice ƴar kallo na zama a filin naɗin sarautar Shehu. Munsha wasan mafarauta sosai ranar, anyi wasannin al'ada masu ban

ƙawa. Da haka taron ya watse, Shehu ya zama sarki, Asiya shugabar mata. Har taro suke gudanarwa, duk ƙarshen wata. Dani da Asiya haka mu kaita hayayyafa. Yarana Huɗu cib, Ɗahiru, Karima, Dauda, Izzatu, Sai tulelen cikin nabiyar. Asiya kuma yaranta Uku namiji ɗaya mata biyu, sai ƙaramin cikin na huɗu. Faɗar wuyar da nasha a wannan shekarun, ba abu bane wanda zai rubutu, aimun afuwa.Amman kallo ɗaya kaimun kasan ina azabtuwa, na tsofe, na bushe, sai hidimar yara nake yi. Ɗahiru kuwa kullum yana ƙunshe a ɗaki, bana bari ya fita, daya fita yara suke tunkuɗeshi ya faɗi har sai yaji rauni, ko suita tuɓe mai wando suna ma halittarshi dariya. Kullum yana biye dani, ko kuma ya zauna a dokin ƙofarmu yaita kallon yara suna wasan ƴar gala_gala a tsakar gida, yaita dariya. Tausayinshi ya cika zuchiyata fam. Shi yasa gabaki ɗaya na maida hankalina zuwa kanshi. Sallar dare kuwa harya zame mun jiki. Babu da irin sharrin da Asiya bata bini ba, amma ina ganin falalar adda'a. Tunda na samu wannan cikin, Asiya ta murɗa kanbunta Shehu bai kuma tako ƙafafunshi da sunan shigowa ɗakin ba. Ga cikin yazo mun da wani irin laulayi, dan harma na gama fidda rai da rayuwar baki ɗaya. In Yara suka shiga ɗakin Asiya, sha Allahu da kuka suke fitowa, yaranta ƙananu harta koya musu, hantarar yayyensu suma.

Ina zaune ina wankin yara. Shehu ya shigo cikin shiga irinta sarakan dawa yace.

"Ke Laila, wancan yaron ya fito, ga mota za'a wuce dasu birni almajirci. Asiya, kema ki kawo naki, Yaya Iyami, yaran duk su fito. Ƙirji na dafe nace.

Sarki shayi ne a jikin yaronnan, a hakan za'a kaishi almajirci? Jijiyar bata warke ba, jiya da yasa wando wallahi ya fame ta har saida tayi jini. Sarki karka tagayyara mun yaro" Nan su Matar Malam su kai ca a kaina. Inaji ina gani, aka fita da Ɗahiru, yana ihun kiran sunana. Ai take na durƙushe na soma naƙudar dole. A kaina aka rufu, nan naita abu guda, wasa gaske har washe gari ban haihu ba. Saida suka ga na kusan macewa aka sani a keken shanu, zuwa Asibiti. Amma Shehu yaƙi zuwa fur, Iyami da matar malam ne suka tafi dani. Ban kuma sanin ina kaina yake ba. Saina farka naga babu ciki a jikina, ashe tiyata akayi mun.yara maza har huɗu aka ciro mun, amman ɗaya ana ciroshi, ko kuka bayyi ba ya rasu. Da Shehu na soma haɗa idanu, yayi zuru yana kallon kyautar da Allah ya bani. Maganar wannan magen ta faɗo mun da tace " Laila uwar maza" har bayan suna muna asibiti, ƴan uwana suna faman hidima dani. Dan tunda Shehu yasa kai ya fice a asibitin bai kuma zuwa ba. Ranar sunan matar Malam tazo nan take shaida mun. Yaran sunci suna. Salisu, Tasi'u Sadisu

Allah ya raya su da imani" Shine abunda nace kawai. Kwananmu tara a asibiti aka sallame mu. Mahaifina shi ya biya komai daya shafi kuɗi, yaimun goma sha tara na arziki, Yaya Nazeefa kuma ta bani ɗiyarta Mama dan su taimaka mun, ita da Karima ta wajena da renon Tawayoyina,tare dasu muka koma gida. Cikin tashin hankali da damuwa naita rainon Tawayoyina, bana samun tallafi da kulawar kowa. Gasu da kuka sosai. Bayan Shekara da tafiyar su Ɗahiru, sai gasu sun dawo ganin gida, a lokacin Tawayoyina har sun soma gudunsu ko'ina. Ɗahiru yayi murna da ganin ƙannenshi. Ya sake yaita wasa a cikinsu yana dariya. Nima raina fari sol da naga Ɗahiru a cikin walwala. Haka rayuwa taita tafiya. Shekaru suka shuɗe sosai, su Tawaye har sun girma suma an kaisu almajirci. Asiya ta hana gaba ta hana baya, duk wata kyautatawa ta hana Shehu yayi mana ni da yara. Su tawaye sun sha azaba sosai a wajan Asiya da yaranta. Kullum a cikin duka da kyara suke.

Ina tsugunne muna dukan shinkafa zamu cireta daga samfurarerta. Sai ga Malam ya shigo.

"Iyami ki kwashi Su Laila ku tafi ƙofar fada. Akwai baƙi da muka samu daga jam'iyyar matan

arewa. Suna buƙatar a taro kan matan ƙauyen. Tun ɗazu ake ta faman yekuwa." Ni dai inata aikina, dan duk wani abun arziki ba'a sani a cikinshi, nima bana cusa kaina. Ɗahiru ne yazo zai kama mana aiki, sai naga jini a bayan rigarshi. Gabana ya yanke ras ya faɗi.

Wannan yaron kaje maza ka sake kayanka" Da sauri ya wuce, ni kuma na bishi da idanu gabana na faɗuwa. Asiya ce ta fito cikin gwalli tace da Iyami.

"Nifa na fito kuzo muje, Yaya Tani kumujenku mana, Laila kema zaki iya tawowa." Ni babu tunani a jikina sam, amman haka na ɗauraye jikina na yafa mayafi muka tafi, na bar su Karima da sauran aikin.

MRS BUKHARI

[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: *_🔥GAWURTATTU UKU🤟2023_*

*_TALLAH TALLAH  TALLA🗣🗣🗣🗣🗣_*

_A HAYYEH SAMAH MATAH💃💃💃💃💃💃_
*Ku shiga wannan link ɗin don zaɓar kaya masu rahusa👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻*
https://chat.whatsapp.com/G6BmHCxso0rDZyWVQGgYYj
----------
No
07067964894

*_INA KUKE MATAN KWARAI MATAN DA SUKA AMSA SUNAN SU NA MATA A DUNIYA KU GARZAYO KUZO M A C DON ZABEN NA KWARAI KI DAURA ASAN KIN DAURA SAI ATAMFA DA LACE DA SHADDA, MATERIAL WITH SHOE'S AND BAG WITH JEWELRIES DAGA MAMAN ANNUR COLLECTION._*
*_ANAN KWALIYA ZATA MAIDA KUDINTA GAREKI,  KIFITO ASAN KIN FITO KIN FASA TARO SAI M.A.C  AKAN FARASHI MAI RAHUSA SAYEN NAGARI MAIDA KUDI GIDA IYA KUDIN KI IYA SHAGALINKI🤝_*
*_TANA KANO TANA AIKAWA KO INA DA IKON ALLAH A CIKIN AMINCIN DA YARDAN UBANGIJI_*
*_YAN UWA INA MASU SON SUYI SANA,A BASU DA JARI  TOH GA DAMA TA SAMU, INJI MAMAN ANUR DON ZAKU IYA DAUKAN KAYAN MU KU TALLATA KU DORA NAKU RIBAN SAMA ZAMU AIKA MAKU KAYA GA MAISHI DA SUNAN KU A DUK INDA CUSTOMER DIN KU YAKE BA TARE DA MUYI SAVING NO BASHI BA KUMA BA ZAISAN BA DAGA WURIN KI KAYAN YA FITO BA TAKEN MU GASKIYA DA AMANA,  MUM ANNUR COLLECTION DA KARAMAR RIBA MUKA DOGARA SABODA NEMAN ALBARKA SAI KUN ZO 👏👏👏👏👏_*
[27/01, 11:04 am] BADI'T IBRAHIM: Gawurtattu uku,zasu buɗe aji na musamman da azumi,don

koyar da girke girke na musamman na azumi don kun san mu mata ƴan adone,wajen yin girki in akace baki iya girki ba to tabbas mijinki fa kullum yana kan hanyar yawon restuarent, sannan idanuwansa suna kan ƴammata saboda ya samu sarauniyar girki, kada ki bari a barki a baya don gwangwaje me gidanki.

Domin nema ƙarin bayani,sai ku tuntuɓi waɗannan numbobin👇🏻👇🏻

07068606171
08104335144
08179523215

💃💃💃💃💃

*🤟GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARA TA 2023🤟*
*_Ina kuke masoyan gawurtattu uku ga su ssun dawo muku da wasu sabbin labaransu a wannan sabuwar shekarar, wannan karon salon gawurtacce ne, ku hanzarto kar ku sake ayi babu ku._*
_Sun shirya tsaf a wannan karon don kawo muku labaran da zakuyi fahari da su, tafiyar mai zafi ce sannan ta musamman._

*_Haziƙai kuma gawurtattu ukun sun shirya ne domin kawo muku gwarazan labaran da zaku yi alfahari da su._*

*MATA IYAYEN GIJI*
_Mrs Bukhari_

*INDA BA ƘASA..!*
_Ummu Maheer_

*KARO ƊAYA...!*
_Ummu Affan_

_LITATTAFAN GABAƊAYA AKAN FARASHI MAI SAUƘI DA RAHUSA 1K_

1 500
2 700
3 1000

_Kai tsaye zaku tura kuɗinku ta wannan account number ɗin._

2212328303
RABIATU BASHIR
Zenith bank

_Don Allah wannan karon ba ma buƙatar katin waya, idan baka da account to kaje POS ka bada 50 kob 100 a cikin kuɗin a turo ta account number please._

_Ƴan ƙasar Niger kai tsaye zaku turo ta nan._ 0706 860 6171

*DOMIN NEMAN ƘARIN BAYANI A TUNTUƁI ƊAYA DAGA CIKIN LAMBOBIN NAN.*

0810 433 4144
0817 952 3215
0706 860 6171

*MUN GODE DA KASANCEWA DA GAWURTATTU UKU A SABUWAR SHEKARAR 2023 SABON SALO SABON TAKU.*

_TEAM GAWURTATTU UKU 2023_
[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: MRS BUKHARI
GAWURTATTU UKU
LAMBA TA ASHIRIN DA UKU

LAILA:
Ƙafafuwa kawai nake jefawa, babu kuzari a jikina. Tunanin daya addabeni, meya kawo jini rigar Ɗahiru? Tani ce ta katsemun tunanina da cewa.

"Ke Laila, kinga Sha'awa ƙawarki sai magana take yi miki fa" Da sauri na juyo na dubi Sha'awa, wani sanyi naji sosai sabida dama sona inje in sameta mu tattauna.

"Lafiya Uwar Tawayoyi?" Haka Sha'awa take kirana. Nace mata.

Sha'awa wannan yaron ne naga jini a bayan rigarshi, shine duk kika ganni a ruɗe haka, naji tsoro sosai. Sha'awa tace.

"Zanje in same shi muji ko lafiya, da mun fito fada zan sa Halima tayo mun kiranshi in tambayeshi duk yanda mu kayi dashi zan tawo in sanar miki." Ajjiyar zuchiya na sauke nannauya, sai na ɗanji sukuni a raina. Danfa danfan mata muka riske a zazzaune a fadar mai gari, an shinshinfiɗa karauni, mata da yaran ƙauyan ni bansan sun kai yawan haka ba. Matan mai gari, suna daga gefe, sa'ilin da baƙin da mu kayi suma suke gefe a zaune. Ga kayayyaki buhu_buhu a gabansu a jibge. Wata mata daga cikin baƙinmu, mai gari yaba damar yin magana. Cikin girma da karamci ta soma bayanin abinda ya kawosu cikin ƙauyannan, da manufar jam'iyyar matan Arewa. Ta ɗaura da bamu asalin cikakken tarihin kafuwar jam'iyyar matan Arewa kamar haka.

"A ranar 27 ga watan mayu na shekarar 1963, wasu tarin mata suka haɗu a gidan mai ɗakin tsohon gwamnan jihar Arewa. Hajiya Asiya Hassan Katsina, da nufin yin ƙwarya_ƙwaryar bikin shan shayi, dan jin daɗinsu. Wanda hakan ya haifar da tattaunawa, gami da shawarwarin da suka samar da JAM'IYYAR MATAN AREWA. Babban maƙasudin wannan ƙungiya shine, rungumar dukkannin wata mace da ke arewacin Najeriya, ba tare da yin la'akari addininta ko ƙabilarta ba. A cokacin da aka kammala tattaunawar da ta haifar da JAM'IYYAR MATAN AREWA, an samar da kwamiti acikin matan da suke gurun, dan sanar ma firimiyan jihar Arewa AHMADU BELLO SARDAUNAN SOKOTO , domun sanar dashi yunƙurin da akayi na samar da JAM'IYYAR MATAN AREWA wacce ta kasance bata siyasa bace. Dan neman shawarwari, da tallafi, gami da sa mata albarka, a matsayinshi na shugaba, kuma babban mutum.

Matan da su ka kasance a wajan taron bikin shan shayin sun haɗa da.

1 Laila dogon yaro.

wacce itace
ta fara kawo wannan shawara dan taimakon matan Arewa.
2 Comfot G Dikko
3 Inna Talib
4Helen Akilu
5 Aishatu Joɗs
6Tuha Shehu
7Mardiyya Liman Chiroma
8Ladi Yusuf Gobir
9Bilewu Yusuf Gobir
10Ambashai Shu'ab
11Asiya Hassan Katsina
12Laraba Tata Askira
13Mary Hamman Maiduguri
14Jummal Baba Jimeta
15Margaret Durlong

A ƙarshe kwamitin da aka kafa sun samu ganin firimiyan jihar Arewa SA AHMADU BELLO a ranar 18 ga watan Yulin shekarar 1968 a gidansa.
Bayan an gabatarma da Sardaunan manufofin Ƙungiya, da kuma irin muradan data ƙunsa ta sanya a gaba, Sardauna ya yi na'am da irin manufofinsu tare da bayyana jin daɗinsa akan wannan ƙungiya. Inda yayi musu fatan alkhairi tare kuma da basu gudunmawar Fam ɗari a matsayin gudunmawa, da kuma yi musu alƙawarin basu filin da za su gina ofishin wannan ƙungiya ta JAM'IYYAR MATAN AREWA. Daga wannan ganawa da aka yi da SA AHMADU BELLO SARDAUNAN SOKOTO, sai kwamitin ya gana da matan gwamnan jihar Arewa SA KASHIM IBRAHIM. Waɗanda su ka kasance a gurin wannan ganawa sun haɗa da.

1Khadija Kashim Ibrahim
2 Ya Halima Kashim Ibrahim
3 Zainab Kashim Ibrahim
4Inna Talib
5Helen Akilu
6 Aishatu joɗa
7Comfort  Dikko
8Kydia  F Zakari
9 Laila dogon yaro

Bayan kammala dukkan wata tattaunawa da akayi da matan gwamna. Sai ɗaya daga cikin matanshi, uwar gida Khadija Kashim Ibrahim,  ta samu gwamna akan wannan lamari. Nan take kuwa gwamna ya amince da wannan ƙoƙarin na matan Arewa. Khadija uwar gidan Gwamna ta kirawo taron ganawa a karon farko, wanda ya gudana a gidan Gwamnati, a ranar 21 ga watan Yuli na shekarar 1963 da misalin ƙarfe huɗun yamma. Jawabin uwargidan Gwamnan ta bayyana matuƙar buƙatar samar da ƙungiyar matan arewacin Najeriya tare kuma da yin farin cikin ganin zaratan mata daga yankin Arewacin ƙasar nan da su ka ɗauki zabarin aikin ciyar da ƙasar nan gaba. A ƙarshen jawabin nata ta yi godiya ga matan da suka samar da wannan Ƙungiya tare da yi musu addu'ar Allah ya dafa musu akan wannan kyakykyawar niya tasu. Bayan kammala taron ne aka tafi domun gudanar da zaɓen shugabannin da za su ɗauki nauyin shugabantar wannan ƙungiya ta JAM'IYYAR MATAN AREWA . An zaɓi shuwagabannin da mataimakansu. Sai justis Muhammad Bello a matsayin lauyan ƙungiya.
Jim da kammala zaɓen shuwagabannin wannan ƙungiya ta matan Arewa, shuwagabannin sun kai ziyarar farko zuwa babban asibitin Kaduna a ranar 1 ga watan Disambar shekarar 1964 daga wannan ziyara aka samar da tunanin samar da gidan Marayu.
An sanar da Firimiyan jihar Arewa wannan tunani, inda ya bayar da filin da  za'a samar da gidan marayun, a titin Dendk da ke cikin garin Kaduna. Daga wannan gidan Marayu jam'iyyar matan Arewa ta samar da makarantun kwana na sakandare, tare da motocin jigilar maido ɗabibai jihohinsu. Wannan ƙungiyar bata gaza ba wajan samar  da asibiti dake garin kaduna, wanda a lokacin kyauta ake duba marasa lafiya, kuma har gobe wannan asibitin yana rayuwa, duk da al'amuran rayuwa sun sauya, yanzu ana ɗan karɓar ƴan kuɗaɗen da basu taka kara sun karya ba. A shugancin Laila dogon yaro ne wannan ci gaba ya samu, danta kasance jarumar mace, mai kishin ganin farin cikin matan Arewa, da ci gabansu.Asibitin Laila dogonyaro ake kiran asibitin. Bayan haka, sai Hajiya Laila dogon yaro ta tara abokan shawararta akayi meeting, a wannan zama ne aka samar da tunanin faɗaɗa wannan ƙungiya zuwa jihohin Arewa,tare da buɗe ofishoshi, da naɗa shuwagabanni bayan hakan ya samu kuma, aka sake yin zama dan ganin ƙungiyar ta yaɗu har zuwa ƙananun hukumomi, tare da fidda shuwagabanni, daga ƙananun hukumomi, sai suma aka basu aikin yaɗa ƙungiyar Jam'iyyan matan Arewa, zuwa ƙauyukan dake kewaye  da ƙananun hukumomin

Taƙaitaccen tarihin Hajiya Laila dogon yaro.

An haife ta ne a birnin Kano a 1944 aka yi mata aure tana da shekaru 13. Hajiya Laila dogon

yaro tana gaba  wajan fafutukar kare hakkin mata, musamman ganin an ilmantar da su. Ta shugabanci majalisar ƙasa ta ƙungiyoyin mata a najeriya wato national conucil of women's societies ( NCWS)  daga 1995. Ta rasu tana da shekara 66 a shekarar 2011. Ina sake jaddada ta'aziyyata ga iyalan wannan baiwar Allah, baya goya marayu.
A yanzu kuma ( Hajiya Rabi Saulawa ke riƙe da muƙamin presedent a cikin jam'iyyar matan Arewa. Kuma ita kanta a tsaye take, dan macace jajirtacciya, tana iya ƙoƙarinta dan ganin farin ciki, da walwalar mata)

Gamu a wannan ƙauye na unguwar alƙali munzo dan mu tallafi mata, kuma a buɗe jam'iyyar matan Arewa, ƙarƙashin gwamitin da muke son mu buɗe. Amman zanba uwar gidan mai garin unguwar alƙali dama ta fitar mana da nagartacciyar mace da take ganin zata jagoranci wannan tafiyar, amman wacce ta zama ta iya karatu da rubutu, sai kuma mataimaka biyu da zasu taimaketa.

Sunana Hajiya Turai  shugabar Jam'iyyar matan Arewa ta ƙaramar hukumar Bakori, tare dani akwai Hajiya Tabawa shugabar jam'iyar matan Arewa ta ƙaramar hukumar Faskari.
Waje yayi tsit, ni dai sai kallon matannan nake, ina jin inama zan iya zama ɗaya daga cikinsu, jibesu tsab_tsab dasu, kuma duk mata ne cikakku da suka san ƴancin kansu. Uwar gidan mai gari ta miƙe tace.
"Ina godiya da wannan karramawar da akayi mun. Sannan ina godiya sosai, kuma ina farin cikin shigowar wannan jam'iyyar matan Arewa cikin wannan gari namu, wani babban alkhairi ne ya shigo mana, Allah ya jiƙan Laila dogon yaro. Allah ya saka ma da (MARYAM ABACHA DA ALKHAIRI) ni a tunanina da nazari na, ina ganin babu wacce ta dace da wannan matsayin kamar Laila Uwar gidan sarkin Mafarauta, dan ta kasance jajirtacciya, mai haƙuri da rashin raki. A garinnan babu iriyar tsangwamar da bata shiga ba, amma sau ɗaya bata taɓa zuwa gaban mai gari ta durƙusa da sunan ƙorafi ba, haka muma da muke sauraron ƙararrakin talakawa, bamu taɓa cin karo da Laila ta kawo ƙarar kowa ba. Kuma matar Malam ta tabbatar mun da haƙuri da juriyar Laila. Sai dai bani da masaniya akan iya rubutu, da karatunta." Gabana ne ya yanke ya faɗi, wani tsoro yayi tsalle ya dira a ƙirjina, nan take sai nake jin kamar numfashina yana kakkatsewa tsabar farin cikine, ko tsabar kaɗuwa, na kasa banbancewa. Wannan baiwar Allahn ta bani damar miƙewa dan jama'a su ganni da kyau. Jikina har wani kakkarwa yake yi, idanu muka haɗa da Shehu wanda ya ɗaga hannu halamar yana da magana.

Mrs Bukhari ce
_TEAM GAWURTATTU UKU 2023_[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: GAWURTATTU UKU
MRS BUKHARI

LAMBA TA ASHIRIN DA HUƊU.

Laila:
Mai gari yaba Shehu damar yin magana.
"Mai gari, wannan matsayi da ake tunanin ba Laila ta kaishi ina? Sannan ba wannan ba, Laila bata iya karatu da rubutu ba sam. Ina ganin ga Asiya a bata, dama ta saba karɓar kuke." Matar

mai gari tace.

"Shehu kaba baƙi damar gudanar da abinda ya kawo su, dan sauri suke yi, sannan Laila ai tana da bakin magana ko, kana tunanin ja da hukuncinane?" Gum Shehu yayi, Asiya sai mugun kallo take danƙara mun. A sannaye nace.

Na iya rubutu da karatu ranki shi daɗe" Ɗaya daga cikin matan jam'iyyar matan Arewa ta miƙo mun form tace in cike ta gani." Hannuna yana kakkarwa na cike form tsab babu kuskure, na miƙa mata. Kallona tayi ta girgiza kai da taga shekaruna. Juyowa tayi tace.

"Daga yau Laila ta zama shugabar matan Jam'iyyar matan Arewa na cikin wannan ƙauyen. Dukkannin wani tallafi da zai shigo ƙauyannan zai shigone ta hannunta. Zamu naɗa wacce zata taimaka mata, dama mataimakiyar mataimakiyarta. Dukkan wani abun inya taso, kona taro kona tallafi, zan turo aimun kiran Laila. Zan ajjiye foms a wajanta, duk mai sha'awar shiga wannan jam'iyyar matan Arewan, sai ya amshi fom a wajan Laila ya cike, akan kuɗi naira biyar. Sannan tunda mun buɗe jam'iyyar matan Arewa a cikin ƙauyannan, ku kuma ku dage ku burunƙasa wannan jam'iyyar, sannan ku ƙirƙiri abubbuwa da dama dan taimakon kanku da kanku. Ga kayan abinci nan, zamu raba ga mata. Bayan uwar gidan mai gari ta kuma zaɓa mana waɗanda zasu taimaki Laila." Ni dai ina tsaye sai hawayen murna nake shatatarwa ba ƙaƙƙautawa. Da Asiya da Shehu kuwa, sun cika fashewa kawai suke jira. Sha'awa aka ciro a matsayin mataimakiyata, sai Iklima amaryar mai gari a matsayin mataimakiyarta. Daga nan suka shiga yi mana rabo. Harda keken ɗinki guda biyu sababbi, da keken saƙa shima biyu. Suka wakiltani akan, in kula a koyama mata sana'a da kekunanan, kuma in sha Allah zasu kawo mana tallafin kekuna masu yawa. Suka bani foms, tare da atampar jam'iyya mai tambarin Arewa a jiki, atampar bulu, Hajiya Turai shigabar jam'iyyar matan Arewa ta  Bakori ta rubuta mun adireshin gidanta, sannan ta bani izinin duk wani abun daya taso, zan iya nemanta kai tsaye" A haka taro ya watse, masu taya ni murna nayi, ƴan baƙin ciki ma sunfi yawa. Sha'awace ta taimaka mun, muka shigar da kekunan gidan mai gari, da sauran mata ƴan uwana. Dan nace a gidan zamu gabatar da koya ma mata ɗinkin. Jiki a saɓule na shiga gidan. Sha'awa kuma ta tsaya a ɗakin Zaure inda Ɗahiru yake ciki.  A tsakar gida na samu Shehu ya kai mari ya kai gwauro. Ina shigowa ya tare ni.

"Ashe munafukace ke Laila, yaushe kika iya rubutu da karatu, ni mijinki ban sani ba?" Wani ƙudidune ya cakeni a ƙahon zuchiyata. Yaci albarkacin Karima data fito da ƙunshin kayanta a zane. Kallona ya koma wajanta, sai naga yaran su Iyami ma duk sun fito da ƙunshin kayansu, duk yanda akayi aikatau za'a tafi dasu birni. Yaran Asiya ma suna can, wata biyu kenan har sun soma yo ma Asiya aike, waccen cin kasuwar data wuce ma harta soma yi musu tarin kayan aure. Mazajen ƙauye da damansu zuchiyarsu ta mace mus, sam basa iya rungumar ɗawainiyar ƴaƴansu, maza a turasu almajirci mata a turasu aikatau, su zasu yi ma kansu kayan ɗaki. Karima tana kuka Shehu ya tusa ƙeyarta, ni kuwa tsabaragen baƙin ciki da takaici na kasa cewa komai, yana fita ya dawo yace ƙanwar Karima ma ta fito ai shingin kaɗan ta isa aure. Ni dai waje na samu na zauna, ina kukan zuchi. Ina zaune sai ga Tani da Zainabu sun fito. Sunai ma matan gida sallama, zasu birni daga can jirginsu zai ɗaga zuwa ƙasa mai tsarki. Nan gidan ya kacame da murna, Amaryar Ɗahiru kuwa tana ɗaki ta kasa fitowa, sabida ba da ita za'aje ba, ya bata haƙuri kam sai wata shekarar. Ɗahiru yana shigowa suka fita, su Baba Mai riga da matar Malam sai binsu da adda'a akeyi, kamar basu san bokanci Ɗahiru yake yi ba. Shehu ne ya shigo gidan da sauri.

"Laila ba zaki yi wannan shugabancin ba, na faɗa miki kenan. Ji mata marasa kunya masu yaƙi da maza, baki isa ki haɗa tafiyarki dasu ba.

Shewar dila kake yi Shehu, in kaga banyi wannan tafiyar ba, bana numfashine a doron ƙasa. Au cigaban nawa ne baka so, sai ci gaban Asiya ɗ'ar gwal ɗinka ko? To kasani nima uwace tai silar zuwana duniya" Kasaƙe Shehu yayi yana kallona, Asiya kuwa ta taso tana huci tace.

"Ki fita idanuna in rufe, dan kinsan nafi ƙarfinki tunda har na sace zuchiyar Shehu a hannunki, kuma na shigo gidan na maisheki bora." Wani irin zabura da nayi saida yasa Asiya taja baya, mari na kawo mata, ta hankaɗo Shehu gaba, ban sani ba na zabga mishi mari. Nan su Baba mai riga suka shiga sallallami, kafin kace me, ita da matar malam, da Iyami, da Laure suka rufu a kaina da duka. Da ƙyar Sha'awa da sauran mata gida suka ƙwaceni, Asiya kuma sai riƙeta Shehu yake yi, wai saita rama mishi marin da nayi mishi. Sha'awace ta jani zuwa cikin ɗakina, ganin yaran du babu yasa na fashe da sabon kuka.

"Haba Laila sai kace wata ƙaramar yarinya. Kiyi haƙuri ai in sha Allah wahalarki ta kusan zuwa ƙarshe, wannan ba komai bane face baƙin ciki, ki tura musu aniyarsu. Yara ki bisu da adda'a a duk inda suke adda'arki zata isa gareki, nima da nawa yara matan aka tafi birnin, to ya zamu yi, a dake mu a hana mu kuka. Ɗahiru kuma mun tattauna dashi, Laila al'adafa yaronnan yake yi, wata uku da farawarshi yace mun. Yanzu haka na baroshi yana murƙususun ciwon mara. Ni a shawarce ki miƙe ku tafi asibitin Bakori a duba shi, shi zaifi. Amman ki jiƙa manda ki bani in kai mishi." Hannu nasa a dai dai saitin ƙirjina na dafe. Dan ji nake kamar zai tarwatse, hawaye kuwa sai wanke mun fuskata yake yi. Namiji da ƙunzugu? Tsarki Allah ya tabbata ga Allah, ɗan Adam ba a bakin komai yake ba. Jikina sai rawa yake yi, manda na jiƙa na bata ta tafi kai mishi. Tana fita Shehu ya shigo wuf.

"Ke Laila baki isa kiyi wannan shugabancin ba na dai faɗa miki, gabaki ɗaya ya dawo kamar wani mahaukaci." Da tsiwa nace.

In kana ganin ba zaka iya barina inyi wannan shugabancin ba, ai saika sauwaƙe mun, kaga ko babu komai na baka filin ɗakin da zaka ƙara wani auren, ka haɗata da Asiya, wala Allah ai ma naɗin sarautar Katsina baki ɗayanta, a sakamakon rabuwa da mai farar ƙafa daka yi, mahaifiyar mata maza." Tsawa ya daka mun, na kalleshi na watsar, nan yaita zazzaga ruwan jaraba, har da mun fatali da kayayyakin aikina, yasa kai ya fice, sai zage_zage yake ta faman yi. Sha'awace ta shigo ta same ni ina kuka. Dafa ni tayi tace.

"Laila ki dakatar da komai, ga kuɗi bari in ranta miki, ku tafi asibiti, ciwon sai tsananta yake, yanzu haka jinine ya ɓalle mai. A gigice na fito da mayafi a kaina, banbi takan kowa ba. Sha'awace ta fito da Ɗahiru, muka ɗauki hanyar Bakori a cikin bodi. Sai yamma lis muka isa asibiti, Ɗahiru ya jiƙe wandonshi sharkab da jini, hawaye naga yana fitarwa ma. Muna shiga asibiti aka ba Ɗahiru gado, ɗan kuɗin da yake hannuna dashi na buɗe fayil, likitoci har sun zo kanshi ana duddubashi, ni dai na haɗe hannayena da kumatuna, na zuba ma sarautar Allah idanu. Bacci yake yi fuskarshi tayi fayau. Wani likita ne ya dubeni yace.

"Mama ki dena damuwa in sha Allah zamu shawo kan matsalar, amman dole zamu kwantar dashi muga yanda yanayin jikin zai kaya. Amman akwai kuɗin magani da zaku biya" A baya na bisu, na biya kuɗin maganin, sannan na nufi gida a ƙagauce nayi musu bayani, sai dai kash mahaifina na samu a kwance a tsakankanin rayuwa da mutuwa, su Yaya Nazeefa da Yaya Salamatu duk an aika sun zo.

"Laila Jafaru harya tafi yayo kiranki, ashe kuma kuna asibiti. Muma asibitin zamu je, dan kwananshi bakwai baya gane ma wanda yake kanshi. Duk muka yi duru_duru, a wajan mahaifina ya cika, rai yayi halinshi. Zaiyana irin tashin hankali da damuwar da muke shiga ɓata lokacine. Kan kace me aka shiga yin shelar mutuwar mahaifinmu, Inna Laraba ce ta kwana da Ɗahiru a asibiti, mu kuma muka kwana munaima mahaifinmu da yayi kwanan keso adda'a. Washe gari aka kaishi gidanshi na gaskiya, da Shehu akaita zaman makoki, babu laifi wannan karon su Asiya da matar malam sun zo. Ana cikin zaman makokinne Baba mai riga Allah yai mata rasuwa itama, sakamakon ciwon ciki na dare ɗaya. Sake ɗunguma can akayi kuma. Ni kuma na koma asibiti.

"Malama Laila wannan yaron sai anyi mishi aiki dangane da lalurar dake damunshi, in ba haka ba, zai dinga yin al'ada duk wata kamar yadda ko wacce mace take yi. Sabida yanayin tsarin halittarshi, a binciken da muka gudanar mun gano ya fi ƙarfi ta ɓangaren maza, Nera dubu talatinne kuɗin aikin. In kuɗin sun samu sai ku dawo mu rubuta muku takadda zuwa babban asibitin cikin gari. Mun sallameku, ya dage yasha maganinshi dukka." Na kiɗima sosai da wannan bayanin da Likita yaimun. Godiya nayi mishi, muka bar asibitin zuwa gida, nan muka ci gaba da karɓar gaisuwar Baba mai riga. Sha'awa da Iklima su ka ci gaba da gudanar da koya ma mata saƙa da ɗinki. Ranar arba'in ɗin mahaifinmu akayi mana rabon gado. Mun tashi da gonakai da shanu, da hatsi cikin rumbu biyu,banda kuɗi tsabarshi. Munyi koke koke sosai da sosai. Ban baro Bakori ba saida na koma asibiti suka rubuta mun takaddar da in munje asibitin birni zamu nuna, sai dai sunce mun sai ƙarshen wata,ishirin ga wata zamu je. Gida na dawo, nan naci gaba da kulawa da matan da ake koyarwa sana'a. Wa'adin da aka ɗibar mana a asibiti yana cika, na ɗauki Ɗahiru muka wuce. Tare da Shehu muka je, nayi mamaki sosai da tsaiwar da Shehu yayi dangane da neman lafiyar Ɗahiru. Mun daɗe sosai a asibiti, dan sai da ya warke tsab ya dawo cikakken namiji, sannan aka sallamemu, muka dawo gida. Haka rayuwa taita garawa, abubbuwa da dama sukaita faruwa, Su Karima sun dawo ganin gida, bayan shekara guda. A lokacin nace ma Shehu yarana bazasu koma birni ba. Yanzu ina da arzikin da zan iya tallafin ƴaƴana. Dan jam'iyyar matan Arewa tayi mun dukkan alkairai, ta dalilin wannan ƙungiyar, naga gwamnonin jihohi da dama, kuma sunyi mana alkhairai masu tarin yawa. A yanzu na zama fitilar dake haskaka gidan Shehu, yaran Asiya duk biyun da ciki suka dawo daga gidan aikinsu. Ni naja gaba aka ƙwato musu hakkinsu, mune har kotu, sun haihu, Asiya taci gaba da rainon yaran shege a gabanta. Rayuwa kenan, haƙuri shine jigon rayuwa, mai haƙuri shike dafa dutse yasha romonshi. Iyayenmu duk Allah yayi musu rasuwa, mun zama dattijai a cikin gidan. Ɗahiru ya zama babban ɗan kasuwar da ake ji dashi, ƙaton shagon atampopine dashi a babbar kasuwa, ya tamfatsa katon gida a cikin ƙauyan unguwar alƙali. Ya ja Su Sabitu ƴan uku, suke taimaka mishi a kasuwa, dan shi kullum a cikin tafiye, tafiye yake. Karima da ƙannenta mata sunyi aurensu, Karima a cikin garin Katsina tayi auren,tana zaune lafiya sumul a gidan mijinta.ƙannen nata kuma duk a ƙauyukan dake maƙwabtaka damu su kai auren. Suna gidajen aurensu cikin rufin asiri. Yaran Asiya mazan na roƙi Ɗahiru ya buɗe musu ƙaramin shagon siyar da takalma a gefen shagonshi. Tunda basu da aikin yi, ga iyalai suna dashi Asiya ranar tayi kuka bana wasa ba, ni naita rarrashinta. Rayuwa tayi mun kyau tayi haske. Ɗahiru yana daga cikin masu taimaka ma matan ƙauyanmu, da Azimi layi sosai ake ja a ƙofar gidanmu, dan Ɗahiru na raba gero da Suger. Ni kuma ina rabon kayan abinci a ƙarƙashin jam'iyyar matan arewa. Babbar matsalata shine, duk su Sabitu sunyi aure, sun hayayyafa. Amman Ɗahiru fur

yaƙi yarda yayi aure, yace zai mutu yana bauta mana, musamman ni. Ranar wata juma'a muka tashi da tashin hankali, Kawu Ɗahiru ne ya fito tsakar gida tsirara, yana ihu yana fisgar gashin kanshi.

"Kayanasu karka kasheni kuskure nayi, nabi Allah na bika, na bika kayanasu" Abunda yaita maimaitawa kenan. Shehu da Lauwali sunyi cirko cirko, sun rasa me zasu yi ma kawu Ɗahiru. Haka muna ji muna gani Ɗahiru ya naɗe kamar alkaki, jini ke zuba a bakinshi dalala. Zaratan yaranane suka Shigo Ɗahiru yana gaba, suna biye dashi a baya. Kamarshi sak da Shehu.

"Baba lafiya meke faruwa haka? Cewar Ɗahiru kenan, yana tambayar Lauwali. Bayani yayi mishi cewar muma gani kawai muka yi yana ihu.' Ihun Ɗahiru ƙaruwa yayi, sai fisge duk wani gashin jikinshi yake yi, wajan na jini, Hannu Ɗahiru yasa ya ciske jelarsa ta fice daga jikinshi. Take ya shiga wani gurnani a take ya mutu, mutuwar tozarci da wulaƙanci, tsirara a gaban kowa da kowa. Su Tani hannu suka ɗaura aka, sukaita xunduma ihu. Ɗahiru ya ja hannuna zuwa cikin ɗakina, dan baya ƙaunar abunda zai ɓata mun rai. Zaunar dani yayi yace.

"Ummi ki dena kuka, bana son ganinki a cikin ko wacce irin damuwa.Bari inyi miki albishir ko zaki ji sanyi. Dan Kawu Ɗahiru kowa yasan mushirikine, ni bazan halarci sallar gawarshi ba ma. Meye bayyiba a gidannan. Babu irin surkullen da baiyi ba a tsakar gidannan. Ajjiyar zuchiya na sauke, haƙiƙa yau zuchiyata ta tsinke, na sake girmama ƙudurar uban giji.

"Ummi bana dani, dake, da Baba da Baba Asiya zamu sauke farali, zakiyi sallah a masallacin ma'aiki. Tsabar farin ciki, hawayene ya soma zuba a idanuna shatata ina godiya ga mahaliccina. Na dubeshi nace.

Allah yaima rayuwarka albarka, ubangiji ya kareka, ya tsareka, Allah yaima albarka, Allah ya sada fuskokinmu a aljannatul firdausi. Amman babban farin cikina shine kayi aure wannan yaron. Shine farin cikina." Hawayenshi ya share yace.

"Ummi wa kike son in aura?"

Jamila yarinyar Yaya Jamila, ita nake son ka aura." Ajjiyar zuchiya ya sauke.

"An gama zanyi aure, amman ku yarda ke da Baba ku tare a gidana dana gina." Nan take na amince mishi. Mutane ƙalilinne suka sallaci gawar Ɗahiru, domun gari kowa yasan Ɗahiru bokanci yake yi. Ya mutu ya bar yaranshi da abun faɗen da baza'a dena faɗeba, sai sanda duniya ta naɗe. Lokaci nayi muka ziyarci ma'aikin Allah. Muna dawowa Ɗahiru yayi aure. Kafin mu dawo Ɗahiru yasa ƙannenshi sun gyara mana waje a cikin tabkeken gidanshi, mai yalwar ɗakuna, anan muka tare, harda Asiya. Amman yaranta maza da iyalansu, suna tsohon gidanmu, da iyalan nasu, sai dai su shigo su gaishemu.Yara matan dake gaban Asiya suma sunyi aure, sabida sun tuba sun nutsu, amman sun jima basu auruba, sun garu, duniya tayi musu atishawa. Rayuwa tayi kyau tayi albarka. Yaƴa rahama ne. Kullum Shehu a cikin rarrashina da tarairayata yake yi. Na zama babbar mace hamshaƙiya. Yaranmu sai jikoki suke tara mana, zuriya tana ta girma tana burunƙasa.

MRS BUKHARI
[08/04, 19:57] Mrs Bukhari: MRS BUKHARI
GAWURTATTU UKU
LAMBA TA ASHIRIN DA BIYAR

ƊANBO:

HINDU:
"Fatsima tasa aka sakeki kuma aka biki da mugun duka haka? Sakin har nawa ne, shegiya kike kuka zaki bada mata" Zainaba ta kalli Hindu tace.
"Saki uku tasa yai mun, wallahi Baba inason mijina nikam" Tsabaragen takaici Hindu rufe Zainaba da mugun duka tayi, tana dukanta tana kuka, itama kukan take yi. Daƙyar su matan gida suka ƙwaceta. Suna cikin haka Audu ya shigo jikinshi a mugun mace mus da takadda a hannunshi. Jagwab ya zauna yana zabgama Hindu wani irin mugun kallon tsana, Zainaba yabi da kallo, yaga bakinta yana zubar da jini. Hawayene suka soma sakkowa a kumatunshi. Bai yi magana ba, ya fice a ɗakin zuwa turakarshi. A canma jagwab ya zauna ya shiga zurfin tunani.
Haƙiƙa shi kanshi yasan yayi zalunci ga Shamsiyya da yaranta, ta yaya zai iya kare kanshi akan abinda yara sukai ƙararshi akai? Shi kanshi ya shiga kogin dana sani, mara madafa, dan yasan Shamsiyya ba zata taɓa mancewa da irin azabtar da'ita da yayi ba. Tunano baya ya soma yi, a lokacin da yake zuwa ƙofar gidansu taɗi, da irin musayar kalaman soyayya da suke yi a tsakaninsu. Abubbuwa iri_iri yaita tunanowa, Hindu da dai taga shirin yayi yawa, sai tabi Audu ɗakinshi, a kwance ta sameshi idanunshi jawur.
"Malam ince dai lafiya ko? Naga ka shigo jiki a mace baka ce mana komai ba, kuma kana ganin Zainaba mijin yayi mata makirin duka, ya rangaɗo mata saki har uku. Ni fa wallahi bazan yarda ba Malam. Dubanta yayi da kyau yace.
"Ai bazan daki ƴar mutane ni ince nawa yaran su sha ba. Gwargwadon yadda zan cutar da ƴar wasu, gwargwadon yanda za'a cutar da nawa yaran. Ta gode Allah ma, da har ta gane gidansu ma. Ki fita ki bani waje ina son hutawa, kuma ki shirya zaman kotu, ki sanar da Shazili ma, su Zaliha sun doka mu a kotu." Wata zabura tayi tasa hannu aka tace.
"Ni Hindu naga ta kaina, kishiya tara rana ɗaya, ta goma na ƙofar gida. Kotu fa kace, anya yarannan yaran sunna ne kuwa? Kai ɗin suka maka a kotu? Nan cikinta ya juya ba shiri ta tsure sai zawo, Audu dai baya iya cewa komai.
Anyi roƙon duniya akam Shamsiyya ta janye ƙarar amman su Shatu sunce basu amince ba. Hindu da Shazili suna cikin tashin hankali.
KOTU:
SHAMSIYYA:
Muna zaune a bakin kotun, muna tsumayar a gama shari'ar dake gaban tamu kafin mu shiga. Hindu da yaranta da ƴan uwanta, suna gefe guda. Nima muna gofe guda, da yara dasu Goggo Rakiya. Audu yana gefe guda shi da abokinshi, ya zabga tagumi. Yayi matuƙar rama, kamar bashi da lafiya ne ma, dan ina gani abokinshi ya zaunar dashi zaune. Saida aka ƙare shari'ar da akeyi sannan alƙalin ya nemi ganawa damu a ofishinshi.
"Barista Zaliha tayi mun bayanin komai, na zaɓi mu tattauna a ofishinane dan kar duniya ta

zagi Audu. Amman Shamsiyya zanso ki bani labarin irin zaluncin da Audu yai miki, karki rage komai, hakkinku dana yaranki za'a kwato miki. Numfasawa nayi, na dubi Audu wanda yake mun kallon inji ƙanshi.  Hindu da Shazali kuwa sai zazzare idanun tsoro suke yi, Shagari, kuwa yayi shiru sai faman jijjiga kai yake yi. Nan na soma zayyanema alƙali irin zaman da mukayi da Audu, da Hindu, da irin zaluncin da sukaimun. Ofishin ya ɗauki shiru, sai hawaye muke sharewa ni da yarana da ƴan uwana. Alƙalinnan na kalla nace.

Ni na yafe musu, ai musu sassauci, babu komai ai duniya ce. Shatu tace.

"Ina da ja ya mai shari'a. Mu munason a kwato mana hakkinmu a wajan mahaifinmu, na kasa kula damu da yayi" Zaliha tace.

"Gaskiya ne yallaɓai muna son a ƙwato mana hakkinmu" Idanu na lumshe, Audu kuwa gabaki ɗaya ya galabaita, sai runtse idanu yake yi. Alƙali ya gama rubuce rubucenshi ya dubi Audu yace.

"Me zaka ce Audu, kana da ja, ko ƙarin bayani a bisa bayanin da Shamsiyya tayi?" Murya na rawa yace.

"Bani da ja yallaɓai. Wallahi duk abinda ta faɗa nayi mata, da sa hannun wannan algungumar matar tawa, wacce take sani a keken ɓera, ta haifamun kangarurrun yaran da suka gagaremu daga ni, har ita. Tabbas bansan komai nasu Shatu da ƴan uwanta ba. Sai dai tsana da tsangwamarsu kaɗai na sani. Bani da bakin da zan roƙi gafararku ƴaƴana, amman ku gafarceni nayi kuskure." Hawaye yake sharewa, harda dafe ƙirji, da dukkan halama ciwo yake ji a zuchiyarshi. Hindu da Shazili suma sai haƙuri suke bayarwa. Alƙali ya umarci Audu da biyana duk wahalhalun da nayi akan ci da sha, da ilmantar mishi da yaranshi da nayi. Sai ai mishi afuwa, ita kuma Hindu tayi alƙawarin ba zata kuma ƙulla wani makircin ba. Shazili kuma akace zaiyi zaman gidan kaso na wata biyu, tare da cin tararshi na dubu talatin. Audu ya amince zai bani gonakanshi duk biyun daya gada. Tare da yin alƙawarin bazai kuma cuta mun ba. Haka dai alƙalinnan mai adalci yai mana sulhu a tsakaninmu. Muka dawo gida. Audu ya ɗebo duk takaddun kadarorinshi ya danƙama su Zaliha. Suka sa hannu suka amsa, sannan suka ɗaukeni daga gidan.

Bamu sake waiwayar ƙauyannan ba, har sai da sha'anin bukukuwansu Shatu ya taso, ni kuma nace dole sai dai ayi bikinnan a gidan mahaifinsu. Shine muka dawo gidan, munzo mun tadda Audu cikin jinya, wujiga_wujiga, duk ya rame ya ƙanjame, sai an tayar sai an ƙwantar. Ina hawaye na dubi Hindu nace.

"Tun yaushe yake fama da wannan ciwon Hindu?" Cikin kuka Hindu tace.

"Watanshi shida cur a kwance, Usman ya koma wajanki a birni babu jimawa ciwon ya kwantar dashi, dama a tsaitsaye yake ta fama da ciwon, tun lokacin da wannan abun ya faru yake fama, kuma barinki gidan ya kuma ɗaga hankalinshi sosai. Wallahi bashi kaɗaiba Shamsiyya ni kaina gidan da ƙauyan baya mun daɗi. Tunda jama'ar ƙauyannan suka ganoni, shikenan fita wannan ta gagareni. Ku yafeni Shatu na tuba. Hawaye na share, na dubi Mariya ƴar gidan Hindu wacce take gidan aure.

Mariya ganin gida kikazo yine, na ganki da yara?" Hindu tace.

"Ummm inji mai ciwon baki. Mijinta ne ya rasu, takaba take yi. Bata gama takabar ba, dangin mijin suka raba gado, aka tasheta a gidan. Tuminin takabarta kawai suka bata, hakkin yaranta na hannun wan mahaifin nasu. Duk haka muke zaune, ga Zainaba  Hannatu ta samu tayi aure da ƙyar, wallahi wuya take ci a gidan Auren. Duka kuwa wane Audu. Ga mijii ba lafiya,

yara mazan kuma. Shagari ta ƴaƴanshi kawai yake yi, wallahi hatsin da zamu saka a bakinmu gagararmu yake yi. Matarshi ta gama asirceshi, sai abinda tace yake yi. Ƙiri_ƙiri take hanashi kulawa damu. Shazali kuma ba sana'a yake yi ba. Gashi da iyali. Shi kuma Muttaƙa ya jijjiga wata sata a birni, shi da abokanshi, yanzu haka maganar nan da nake miki yana gidan gyaran hali a birni. Wai saiya shekara ashirin za'a sakoshi." Kuka suke yi dukkansu, suna roƙon gafarar ƴan uwan nasu. Ajjiyar zuchiya na sauke.

Allah ya kyauta, yanzu shi Audu an kaishi asibiti ne?" A kunyace Hindu tace.

